وَبَدَا لَهُمْ سَيِّئَاتُ مَا عَمِلُوا وَحَاقَ بِهِم مَّا كَانُوا بِهِ يَسْتَهْزِئُونَ
٣٣ وَقِيلَ الْيَوْمَ نَنسَاكُمْ كَمَا نَسِيتُمْ لِقَاءَ يَوْمِكُمْ هَٰذَا وَمَأْوَاكُمُ النَّارُ
وَمَا لَكُم مِّن نَّاصِرِينَ ٣٤ ذَٰلِكُم بِأَنَّكُمُ اتَّخَذْتُمْ آيَاتِ اللَّهِ هُزُوًا
وَغَرَّتْكُمُ الْحَيَاةُ الدُّنْيَا ۚ فَالْيَوْمَ لَا يُخْرَجُونَ مِنْهَا وَلَا هُمْ يُسْتَعْتَبُونَ
٣٥ فَلِلَّهِ الْحَمْدُ رَبِّ السَّمَاوَاتِ وَرَبِّ الْأَرْضِ رَبِّ الْعَالَمِينَ ٣٦
وَلَهُ الْكِبْرِيَاءُ فِي السَّمَاوَاتِ وَالْأَرْضِ ۖ وَهُوَ الْعَزِيزُ الْحَكِيمُ ٣٧

ترتيبها ٤٦ سُورَةُ الأَحْقَافِ آياتها ٣٥

بِسْمِ اللَّهِ الرَّحْمَٰنِ الرَّحِيمِ

حم ١ تَنزِيلُ الْكِتَابِ مِنَ اللَّهِ الْعَزِيزِ الْحَكِيمِ ٢ مَا خَلَقْنَا (الجزء ٢٦ الحزب ٥١)
السَّمَاوَاتِ وَالْأَرْضَ وَمَا بَيْنَهُمَا إِلَّا بِالْحَقِّ وَأَجَلٍ مُّسَمًّى ۚ وَالَّذِينَ
كَفَرُوا عَمَّا أُنذِرُوا مُعْرِضُونَ ٣ قُلْ أَرَأَيْتُم مَّا تَدْعُونَ مِن
دُونِ اللَّهِ أَرُونِي مَاذَا خَلَقُوا مِنَ الْأَرْضِ أَمْ لَهُمْ شِرْكٌ فِي
السَّمَاوَاتِ ۖ ائْتُونِي بِكِتَابٍ مِّن قَبْلِ هَٰذَا أَوْ أَثَارَةٍ مِّنْ عِلْمٍ إِن كُنتُمْ
صَادِقِينَ ٤ وَمَنْ أَضَلُّ مِمَّن يَدْعُو مِن دُونِ اللَّهِ مَن
لَّا يَسْتَجِيبُ لَهُ إِلَىٰ يَوْمِ الْقِيَامَةِ وَهُمْ عَنْ دُعَائِهِمْ غَافِلُونَ ٥



**(33) Munanan abubuwan da suka aikata a duniya na kafirci da sava suka bayyana a gare su, kuma azaba ta sauka a kansu, wadda suka kasance suna yi izgili a kanta yayin da ake tsoratar da su ita.**
**(34) Kuma Allah ya ce da su: "Yau zamu qyale ku a cikin wuta kamar yadda kuka manta da haxuwa da wannan rana, don haka baku yi mata tanadin imani da aiki nagari ba, matabbatar ku da zaku tare a ciki ita ce wuta, kuma baku da wasu mataimaka da za su kare ku daga azabar Allah".**
**(35) Wannan azabar da ake yi muku, saboda kun riqi ayoyin Allah ne abin izgili, kuna izgili da su, kuma rayuwa ta yaudare ku da kayan jin daxinta da sha'awarta, to a yau waxannan kafirai masu yin izgili da ayoyin Allah ba za su fita daga wuta ba, za su wanzu a cikinta, suna masu dauwama har abada, kuma ba za a komar da su rayuwar duniya ba, ballantana su yi aiki nagari, kuma ubangijin su ba zai yarda da su ba.**
**(36) Ga Allah kaxai godiya ta tabbata, Ubangijin sammai, kuma Ubangijin qassai, kuma Ubangijin dukkan halitta.**
**(37) Kuma girma da xaukaka duk nasa ne, a cikin sammai da qassai, kuma shi ne mabuwayin da ba wanda yake galaba a kansa, mai hikima a halittarsa, da tsarawarsa, da gudanarwarsa da kuma shari'arsa.**

# Suratul Ahqaf

An Saukar Da Ita A Makkah

## Daga Manufofin Surar:

**Tsayar da hujja a kan masu qaryatawa, da kuma gargaxin su da azaba, don haka kalmar gargaxi ta maimaitu a cikin Surar.**

## Tafsir:

**(1) (Haa Mim) Bayanin ire-iren waxannan haruffai ya gabata a farkon suratul Baqara.**
**(2) Saukar da Alqur'ani daga Allah, Mabuwayin da ba wanda yake rinjayarsa, kuma mai hikima a cikin halittarsa, da qaddarawarsa, da kuma shari'arsa.**
**(3) Ba mu halicci sammai, da qassai da abin da yake tsakaninsu don wasa ba, a'a mun halicce su ne gaba xaya bisa gaskiya, kuma don wata hikima mai girma, daga ciki akwai bayi su san Allah ta hanyarsu, sai su bauta masa shi kaxai, ba zasu yi shirka da shi ba, kuma don su tsaya da abubuwan da aka sanya su halifofi a bayan qasa don shi, har zuwa wani lokaci qayyadadde da Allah ne kaxai ya san shi. Waxanda suka kafircewa Allah, masu bijirewa ne ga abin da ake yi musu gargaxi da shi a littafin Allah, basa kula da shi.**
**(4) Ya kai wannan Manzo, ka faxa wa waxannan mushirikai, masu bijirewa gaskiya: "Ku ba ni labarin gumakan ku, waxanda kuke bautawa koma bayan Allah, me suka halitta daga cikin qasa? Shin sun halicci dutse? Ko sun halicci qorama? Ko suna da wani rabo ko tarayya da Allah cikin halittar sammai? Ku kawo min wani littafi da aka saukar daga wurin Allah gabanin Alqur'ani, ko wani ragowar ilimi da magabata na farko suka bari, in gaskiya kuke kai cikin da'awarku na cewa gumanku sun cancanta a bauta musu.**
**(5) Babu wanda ya fi vata fiye da wanda yake bautawa gunki koma bayan Allah, gunkin da baya amsa kiransa har zuwa har alqiyama. Waxannan gumaka da suke ta bauta musu koma bayan Allah rafkanannu ne daga kiran da masu bauta musu suke yi musu, ballantana su amfane su ko su cutar da su.**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Yin izgili da ayoyin Allah kafirci ne. 2 - Haxarin ruxuwa da daxin duniya, da kayan sha'awar cikinta.**
**3 - Tabbatuwar siffar girma ga Allah Maxaukakin Sarki. 4 - Amsa addu'a tana cikin mafi bayyanar dalilai da suke nuna samuwar Allah da cancantarsa da bauta.**

وَإِذَا حُشِرَ ٱلنَّاسُ كَانُوا۟ لَهُمْ أَعْدَآءً وَكَانُوا۟ بِعِبَادَتِهِمْ كَٰفِرِينَ ٦ وَإِذَا
تُتْلَىٰ عَلَيْهِمْ ءَايَٰتُنَا بَيِّنَٰتٍ قَالَ ٱلَّذِينَ كَفَرُوا۟ لِلْحَقِّ لَمَّا جَآءَهُمْ هَٰذَا
سِحْرٌ مُّبِينٌ ٧ أَمْ يَقُولُونَ ٱفْتَرَىٰهُ ۖ قُلْ إِنِ ٱفْتَرَيْتُهُۥ فَلَا تَمْلِكُونَ
لِى مِنَ ٱللَّهِ شَيْـًٔا ۖ هُوَ أَعْلَمُ بِمَا تُفِيضُونَ فِيهِ ۖ كَفَىٰ بِهِۦ شَهِيدًۢا بَيْنِى
وَبَيْنَكُمْ ۖ وَهُوَ ٱلْغَفُورُ ٱلرَّحِيمُ ٨ قُلْ مَا كُنتُ بِدْعًا مِّنَ ٱلرُّسُلِ
وَمَآ أَدْرِى مَا يُفْعَلُ بِى وَلَا بِكُمْ ۖ إِنْ أَتَّبِعُ إِلَّا مَا يُوحَىٰٓ إِلَىَّ وَمَآ أَنَا۠
إِلَّا نَذِيرٌ مُّبِينٌ ٩ قُلْ أَرَءَيْتُمْ إِن كَانَ مِنْ عِندِ ٱللَّهِ وَكَفَرْتُم بِهِۦ
وَشَهِدَ شَاهِدٌ مِّنۢ بَنِىٓ إِسْرَٰٓءِيلَ عَلَىٰ مِثْلِهِۦ فَـَٔامَنَ وَٱسْتَكْبَرْتُمْ ۖ
إِنَّ ٱللَّهَ لَا يَهْدِى ٱلْقَوْمَ ٱلظَّٰلِمِينَ ١٠ وَقَالَ ٱلَّذِينَ كَفَرُوا۟
لِلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ لَوْ كَانَ خَيْرًا مَّا سَبَقُونَآ إِلَيْهِ ۚ وَإِذْ لَمْ يَهْتَدُوا۟ بِهِۦ
فَسَيَقُولُونَ هَٰذَآ إِفْكٌ قَدِيمٌ ١١ وَمِن قَبْلِهِۦ كِتَٰبُ مُوسَىٰٓ
إِمَامًا وَرَحْمَةً ۚ وَهَٰذَا كِتَٰبٌ مُّصَدِّقٌ لِّسَانًا عَرَبِيًّا لِّيُنذِرَ
ٱلَّذِينَ ظَلَمُوا۟ وَبُشْرَىٰ لِلْمُحْسِنِينَ ١٢ إِنَّ ٱلَّذِينَ قَالُوا۟ رَبُّنَا
ٱللَّهُ ثُمَّ ٱسْتَقَٰمُوا۟ فَلَا خَوْفٌ عَلَيْهِمْ وَلَا هُمْ يَحْزَنُونَ ١٣
أُو۟لَٰٓئِكَ أَصْحَٰبُ ٱلْجَنَّةِ خَٰلِدِينَ فِيهَا جَزَآءًۢ بِمَا كَانُوا۟ يَعْمَلُونَ ١٤



**(6) Kuma tare da cewa gumaka baza su amfanar da su ba a nan duniya, to haka ma idan aka tara su a ranar alqiyama, za su zamo maqiya ga masu bauta musu, su barranta daga gare su, kuma su yi musun sun san suna bauta musu.**
**(7) Idan ana karanta musu ayoyinmu waxanda aka saukar ga Annabinmu, sai waxanda suka kafirce su ce dangane da Alqur'ani, yayin da ya zo musu a hannun Manzonsu: "Wannan tsafi ne a fili, ba wahayi ba ne daga Allah".**
**(8) Shin waxannan mushirikai suna cewa: "Annabi Muhammad ne ya qirqiri wannan Alqur'ani, ya dangana shi ga Allah?". To ka gaya musu - Ya kai wannan Manzo -: "Idan har ni ne da kaina na qirqire shi, to ai baku da wata dabara a kaina in Allah ya yi nufin azabtar da ni, don haka ta yaya zan bijirar da kaina ga azabar Allah, ta hanyar qirqira masa qarya?!" Allah kaxai ya san abin da kuke kutsawa cikinsa na suka ga Alqur'aninsa da kuma gare ni, kuma ya isa ya zamo mai shaida a tsakanin ni da ku, kuma shi mai yawan gafarta zunuban wanda ya tuba zuwa gare shi daga cikin bayinsa, kuma mai jinqan su.**
**(9) Ya kai wannan Manzo, ka faxawa waxannan mushirikai, masu qaryata Annabtar ka cewa: "Ba ni ne farkon Manzo da Allah ya aiko shi ba, ballantana ku yi mamaki kiran da nake muku, Manzanni masu yawa sun riga ni, kuma ban san me Allah zai yi da ni ba, haka nan abin da zai yi da ku a duniya, ba komai nake bi ba, face abin da Allah ya yi min wahayi, bana faxa, ko in aikata, sai daidai da abin da ya yi min wahayi, kuma ni ba kowa ba ne face mai yin gargaxi, ina gargaxin ku azabar Allah, gargaxi bayyananne.**
**(10) Ya kai wannan Manzo, ka cewa waxannan mushirikai: "Ku ba ni labari mana, idan wannan Alqur'ani daga wajen Allah yake, amma kuka kafirce da shi, kuma wani mai shaida daga cikin bani-isra'ila ya shaida a kan cewa daga wurin Allah yake, dogaro da abin da ya zo a cikin Attaura a kansa, kuma shi ya yi imani da shi, amma ku kuka yi girman kai ga barin yin imani da shi, ashe baku zama azzalumai da hakan ba?!. Haqiqa Allah baya datar da mutane azzalumai ga fahimtar gaskiya. (11) Waxanda suka kafirce wa Alqur'ani, da abin da Manzonsu ya zo da shi suka cewa waxanda suka yi imani: "Da abin da Muhammad ya zo da shi gaskiya ne, kuma yana shiryarwa zuwa ga alheri, da waxannan talakawan da bayi da raunana basu riga mu zuwa gare shi ba. Tunda basu shiriya zuwa abin da Manzonsu ya zo da shi ba zasu ce: "Wannan abin da ya zo mana da shi qarya ce daxaxxiya, mu kuma bama bin qarya". (12) Gabanin wannan Alqur'ani akwai Attaura, littafin da Allah ya saukar da shi ga Annabi Musa (A.S) kuma jagora ne ana koyi da shi cikin gaskiya, kuma rahama ne ga wanda ya yi imani da shi, ya yi masa biyayya daga cikin bani-isra'ila. Wannan Alqur'ani wanda aka saukar ga Annabi Muhammad (S.A.W) littafi ne mai gasgata littafan da suka gabace shi, kuma ya zo cikin harshen larabci, domin ya gargaxi waxanda suka zalunci kansu, ta hanyar yin shirka da Allah, da aikata savo. Kuma shi bushara ne ga masu kyautatawa, waxanda suka kyautata dangantakarsu da Mahaliccinsu, da dangantakarsu da halittar Allah. (13) Haqiqa waxanda suka ce: "Ubangijin mu shi ne Allah, ba mu da wani Ubangiji sai shi, sannan suka daidaita a kan imani da aiki nagari, to babu tsoro a kansu cikin abin da suke fuskanta a lahira, kuma ba za su yi baqin ciki a kan abin da ya wuce su na rabon duniya ba, ko kuma abin da suka bari a bayansu. (14) Waxanda suka siffantu da waxancan siffofi, su ne 'yan Aljannah, masu zama a cikinta har abada, sakamako a kan ayyukansu na qwarai, waxanda suka gabatar da su a duniya.**

**Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa: 1 - Duk abin da aka bautawa koma bayan Allah, to zai yi Allah wadarai da wanda ya bauta masa daga cikin kafirai. 2 - Annabi bai san gaibu ba, sai iya abin da Allah ya tsinkayar da shi. 3 - Samuwar abin da yake tabbatar da Annabcin Manzonmu (S.A.W) a ciki littafan da suka gabata. 4 - Bayanin falalar tsayawa a kan addini, da sakamakon ma'abotanta.**

وَوَصَّيۡنَا ٱلۡإِنسَٰنَ بِوَٰلِدَيۡهِ إِحۡسَٰنًاۖ حَمَلَتۡهُ أُمُّهُۥ كُرۡهٗا وَوَضَعَتۡهُ
كُرۡهٗاۖ وَحَمۡلُهُۥ وَفِصَٰلُهُۥ ثَلَٰثُونَ شَهۡرًاۚ حَتَّىٰٓ إِذَا بَلَغَ أَشُدَّهُۥ وَبَلَغَ
أَرۡبَعِينَ سَنَةٗ قَالَ رَبِّ أَوۡزِعۡنِيٓ أَنۡ أَشۡكُرَ نِعۡمَتَكَ ٱلَّتِيٓ أَنۡعَمۡتَ
عَلَيَّ وَعَلَىٰ وَٰلِدَيَّ وَأَنۡ أَعۡمَلَ صَٰلِحٗا تَرۡضَىٰهُ وَأَصۡلِحۡ لِي فِي ذُرِّيَّتِيٓۖ
إِنِّي تُبۡتُ إِلَيۡكَ وَإِنِّي مِنَ ٱلۡمُسۡلِمِينَ ١٥ أُوْلَٰٓئِكَ ٱلَّذِينَ نَتَقَبَّلُ
عَنۡهُمۡ أَحۡسَنَ مَا عَمِلُواْ وَنَتَجَاوَزُ عَن سَيِّـَٔاتِهِمۡ فِيٓ أَصۡحَٰبِ
ٱلۡجَنَّةِۖ وَعۡدَ ٱلصِّدۡقِ ٱلَّذِي كَانُواْ يُوعَدُونَ ١٦ وَٱلَّذِي قَالَ
لِوَٰلِدَيۡهِ أُفّٖ لَّكُمَآ أَتَعِدَانِنِيٓ أَنۡ أُخۡرَجَ وَقَدۡ خَلَتِ ٱلۡقُرُونُ مِن
قَبۡلِي وَهُمَا يَسۡتَغِيثَانِ ٱللَّهَ وَيۡلَكَ ءَامِنۡ إِنَّ وَعۡدَ ٱللَّهِ حَقّٞ فَيَقُولُ
مَا هَٰذَآ إِلَّآ أَسَٰطِيرُ ٱلۡأَوَّلِينَ ١٧ أُوْلَٰٓئِكَ ٱلَّذِينَ حَقَّ عَلَيۡهِمُ ٱلۡقَوۡلُ
فِيٓ أُمَمٖ قَدۡ خَلَتۡ مِن قَبۡلِهِم مِّنَ ٱلۡجِنِّ وَٱلۡإِنسِۖ إِنَّهُمۡ كَانُواْ خَٰسِرِينَ
١٨ وَلِكُلّٖ دَرَجَٰتٞ مِّمَّا عَمِلُواْۖ وَلِيُوَفِّيَهُمۡ أَعۡمَٰلَهُمۡ وَهُمۡ لَا يُظۡلَمُونَ
١٩ وَيَوۡمَ يُعۡرَضُ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ عَلَى ٱلنَّارِ أَذۡهَبۡتُمۡ طَيِّبَٰتِكُمۡ فِي حَيَاتِكُمُ
ٱلدُّنۡيَا وَٱسۡتَمۡتَعۡتُم بِهَا فَٱلۡيَوۡمَ تُجۡزَوۡنَ عَذَابَ ٱلۡهُونِ بِمَا كُنتُمۡ
تَسۡتَكۡبِرُونَ فِي ٱلۡأَرۡضِ بِغَيۡرِ ٱلۡحَقِّ وَبِمَا كُنتُمۡ تَفۡسُقُونَ ٢٠

**(15) Mun umarci mutun umarni mai qarfi ya kyautatawa mahaifansa, ta hanyar ya yi musu biyayya a rayuwarsu, da bayan mutuwarsu, da abin da bai savawa shari'a ba, Musamman ma mahaifiyarsa, wadda ta xau cikinsa cikin wahala, ta kuma haife shi cikin wahala. Tsawon lokacin xaukan cikinsa har zuwa fara yayensa: wata talatin ne. Har lokacin da ya kai cikar qarfin jikinsa da hankalinsa, ya cika shekara arba'in sai ya ce: "Ya ubangiji ka kimsa min godiya akan ni'imarka a kaina, da iyayena, kuma ka kimsa min in yi aiki nagari, da zaka yarda da shi, kuma ka karve shi daga wurina, kuma kashirya min 'ya'yana, haqiqa ni na tuba gare ka daga laifukana, kuma ni ina cikin masu yin biyayya ga xa'arka, masu sallamawa ga umarninka.**

**(16) Waxannan su ne muke karvar mafi kyawun abin da suka aikata daga kyawawan ayyukansu, kuma muke yafe musu laifukansu, ba ma kama su da su, kuma suna cikin 'yan Aljannah. Wannan alqawarin da a ka yi musu, alqawari ne na gaskiya, tabbas zai kasance babu makawa.**

**Yayin da Allah ya ambaci misalin mai bin iyayensa, don kwaxaitarwa a kan bin su, sai kuma ya ambaci misalin mai savawa iyaye, don tsoratarwa akan sava musu, ya ce:**

**(17) Wanda ya cewa iyayensa: "Tir da ku, yanzu kuna yi min alqawarin fitowa daga qabarina a raye bayan na mutu, alhali shekaru aru aru sun wuce, mutane sun mutu a cikinsu, amma babu wanda aka tayar da rai daga cikinsu?! Iyayensa suna neman taimakon Allah ya shiryi xansu zuwa ga imani, suna cewa xan su: "Halaka ta tabbata a kanka idan baka yi imani da tashin bayan mutuwa ba, don haka ka yi imani. Haqiqa alqawarin Allah na tashi bayan mutuwa gaskiya ne, babu kokwanto a cikinsa. Sai ya ce – yana mai qara maimaita inkarinsa da tashi bayan mutuwa -: "Wannan abin da ake faxa game da tashi bayan mutuwa ba komai ba ne sai labaran da aka ciro daga littafan waxanda suka gabata, da abin da suka rubuta, bai tabbata daga Allah ba".**

**(18) Waxannan su ne waxanda azaba ta tabbata a kansu, cikin al'ummun da suka gabace su daga mutane da aljanu, haqiqa sun kasance tavavvu, ta inda suka yi asarar kawunansu da iyalansu, ta hanyar shiga wuta.**

**(19) Dukkan vangarorin biyu, vangaren 'yan Aljannah, da vangaren 'yan wuta, suna da matakai gwargwadon ayyukansu, matakan 'yan Aljannah matakai ne maxaukaka, matakan 'yan wuta kuwa qasa ne zuwa qasa. Don Allah ya cika musu sakamakon ayyukansu, ba a zaluntar su ranar alqiyama, ta hanyar rage kyawawan ayyukansu, ko qara munanan ayyukansu.**

**(20) Ranar da za a bijirar da waxanda suka kafirce wa Allah, suka qaryata Manzanninsa ga wuta, don azabtar da su a cikinta, kuma za a ce musu cikin zargi da tsawatarwa: "Kun tafiyar da jin daxinku a rayuwar duniya, kun ji daxi da abin da yake cikinta na kayan jin daxi, amma a yau za a saka muku da azabar da zata wulaqanta ku ta qasqanta ku, saboda girman kanku a bayan qasa ba tare da wani haqqi ba, da kuma rashin biyayya ga Allah, ta hanyar aikata kafirci da savon Allah.**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Bayanin matsayin bin iyaye a cikin musulunci, musamman haqqin mahaifiya, da kuma tsoratarwa ga barin sava musu.**

**2 - Bayanin haxarin yalwata wa a cikin jin daxin duniya, saboda tana shagaltarwa daga lahira.**

**3 - Bayanin mummunan narko ga ma'abota girman kai da fasiqanci.**

الحزب ٥١

۞ وَٱذْكُرْ أَخَا عَادٍ إِذْ أَنذَرَ قَوْمَهُۥ بِٱلْأَحْقَافِ وَقَدْ خَلَتِ ٱلنُّذُرُ
مِنۢ بَيْنِ يَدَيْهِ وَمِنْ خَلْفِهِۦٓ أَلَّا تَعْبُدُوٓا۟ إِلَّا ٱللَّهَ إِنِّىٓ أَخَافُ عَلَيْكُمْ
عَذَابَ يَوْمٍ عَظِيمٍ ﴿٢١﴾ قَالُوٓا۟ أَجِئْتَنَا لِتَأْفِكَنَا عَنْ ءَالِهَتِنَا فَأْتِنَا
بِمَا تَعِدُنَآ إِن كُنتَ مِنَ ٱلصَّٰدِقِينَ ﴿٢٢﴾ قَالَ إِنَّمَا ٱلْعِلْمُ عِندَ ٱللَّهِ
وَأُبَلِّغُكُم مَّآ أُرْسِلْتُ بِهِۦ وَلَٰكِنِّىٓ أَرَىٰكُمْ قَوْمًا تَجْهَلُونَ ﴿٢٣﴾ فَلَمَّا
رَأَوْهُ عَارِضًا مُّسْتَقْبِلَ أَوْدِيَتِهِمْ قَالُوا۟ هَٰذَا عَارِضٌ مُّمْطِرُنَا ۚ
بَلْ هُوَ مَا ٱسْتَعْجَلْتُم بِهِۦ ۖ رِيحٌ فِيهَا عَذَابٌ أَلِيمٌ ﴿٢٤﴾ تُدَمِّرُ كُلَّ
شَىْءٍۭ بِأَمْرِ رَبِّهَا فَأَصْبَحُوا۟ لَا يُرَىٰٓ إِلَّا مَسَٰكِنُهُمْ ۚ كَذَٰلِكَ نَجْزِى
ٱلْقَوْمَ ٱلْمُجْرِمِينَ ﴿٢٥﴾ وَلَقَدْ مَكَّنَّٰهُمْ فِيمَآ إِن مَّكَّنَّٰكُمْ فِيهِ
وَجَعَلْنَا لَهُمْ سَمْعًا وَأَبْصَٰرًا وَأَفْـِٔدَةً فَمَآ أَغْنَىٰ عَنْهُمْ سَمْعُهُمْ
وَلَآ أَبْصَٰرُهُمْ وَلَآ أَفْـِٔدَتُهُم مِّن شَىْءٍ إِذْ كَانُوا۟ يَجْحَدُونَ بِـَٔايَٰتِ
ٱللَّهِ وَحَاقَ بِهِم مَّا كَانُوا۟ بِهِۦ يَسْتَهْزِءُونَ ﴿٢٦﴾ وَلَقَدْ أَهْلَكْنَا
مَا حَوْلَكُم مِّنَ ٱلْقُرَىٰ وَصَرَّفْنَا ٱلْءَايَٰتِ لَعَلَّهُمْ يَرْجِعُونَ ﴿٢٧﴾
فَلَوْلَا نَصَرَهُمُ ٱلَّذِينَ ٱتَّخَذُوا۟ مِن دُونِ ٱللَّهِ قُرْبَانًا ءَالِهَةًۢ ۖ
بَلْ ضَلُّوا۟ عَنْهُمْ ۚ وَذَٰلِكَ إِفْكُهُمْ وَمَا كَانُوا۟ يَفْتَرُونَ ﴿٢٨﴾



**(21) Ya kai wannan Manzo, ka ambaci Annabi Hudu xan uwan Adawa a cikin nasaba, yayin da ya yi wa mutanensa gargaxin afkuwar azabar Allah a kansu, alhali suna cikin gidajensu a garin Ahqaf, kudancin tsibirin larabawa, kuma Manzanni sun shuxe, suna yi wa mutanensu gargaxi gabanin Annabi Hudu da bayansa, suna cewa mutanensu: "Kada ku bautawa kowa sai Allah, shi kaxai, kada ku bautawa wani tare da shi, ya ku mutanena ina ji muku tsoron azabar wata rana mai girma, ita ce ranar alqiyama.**

**(22) Sai mutanensa suka ce da shi: "Shin ka zo ne don ka kawar da mu daga bautar allolinmu?! Ba zaka samu haka ba, ka zo mana da abin da kake mana alqawari na azaba, in ka kasance mai gaskiya a cikin abin da kake da'awa".**

**(23) Sai ya ce: "Sanin lokacin azaba yana wurin Allah, ni ban da sani ba, kaxai ni Manzo ne, ina isar muku da saqon da aka aiko shi da shi, sai dai ina ganinku mutane ne da suka jahilci abin da zai amfane ku, don haka sai kuka bar shi, kuka jahilci abin da zai cutar da ku, sai kuka je masa.**

**(24) Yayin da abin da suka yi ta gaggawar ya zo musu na azaba ya zo musu, suka gan shi girgije ya tokare sama, ya fuskanci kwarinsu, sai suka ce: "Wannan girgije zai shayar da mu ruwan sama". Sai Annabi Hudu ya ce musu: "Lamarin ba kamar yadda kuke zato ba ne, cewa girgije ne da zai muku ruwan sama, a'a azabar da kuke ta gaggawar a kawo muku ita ce, iska ce a cikinta akwai azaba mai raxaxi.**

**(25) Tana rusa komai idan ta bi ta kansa, daga abin da Allah ya umarce ta da ta halaka shi, sai suka wayi gari halakakku, ba a ganin komai sai gidajensu, waxanda suka zauna cikinsu, suna matsayin shaida a kan da suna nan a cikinsu. Irin wannan sakamakon mai ciwo, haka muke sakawa masu laifi, waxanda suke zarcewa a kan kafircinsu da savonsu.**

**(26) Haqiqa mun bawa mutanen Annabi Hudu dalilai na tabbata da kafuwa, wanda ba mu ba ku irinsu ba, muka sanya musu ji da suke saurara da shi, da idanu da suke gani da su, da zukata da suke hankalta da su, amma jinsu da ganinsu da hankulansu ba su wadatar musu da komai ba, ba su kare musu azabar Allah ba a yayin da ta zo musu, domin sun kasance suna kafirce wa ayoyin Allah, kuma abin da suke yin izgilanci a kansa na azaba ya sauka a kansu, wanda Annabinsu Hudu yake gargaxinsu a kansa.**

**(27) Haqiqa mun halakar da alqaryun da suke kewaye da ku – Ya ku mutanen Makka -. Haqiqa mun halakar da Adawa, da Samudawa, da mutanen Annabi luxu, da mutanen Madyana, mun nau'anta musu hujjoji da dalilai, ko sa bar kafircinsu su dawo kan gaskiya.**

**(28) Ina ma gumakan da suka riqa alloli koma bayan Allah, suke kusantar su da bauta da yanka sun taimake su?! ba su taimake su ba ko kaxan, sun ma vuya daga gare su a lokacin da suka fi buqatar su. Wannan kuwa shi ne qire da qaryar da suka ci burinta ga kawunansu, na cewa waxannan gumaka za su amfane su, su cece su a wurin Allah.**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Manzanni ba su da wani ilimi na gaibu, sai abin da Allah ya sanar da su kawai.**

**2 - Ruxuwar da mutanen Annabi Hudu suka yi, lokacin da suke zaton wannan girgijen ruwan sama zai shayar da su, don haka ba su tuba ba gabanin ya shammace su.**

**3 - Adawa sun fi quraishawa qarfi, amma tare da haka Allah ya halakar da su.**

**4 - Mai hankali shi ne wanda yake wa'azantuwa da waninsa, jahili kuwa shi ne wanda yake wa'azantuwa da kansa.**

وَإِذْ صَرَفْنَآ إِلَيْكَ نَفَرًا مِّنَ ٱلْجِنِّ يَسْتَمِعُونَ ٱلْقُرْءَانَ فَلَمَّا
حَضَرُوهُ قَالُوٓا۟ أَنصِتُوا۟ ۖ فَلَمَّا قُضِىَ وَلَّوْا۟ إِلَىٰ قَوْمِهِم مُّنذِرِينَ
﴿٢٩﴾ قَالُوا۟ يَٰقَوْمَنَآ إِنَّا سَمِعْنَا كِتَٰبًا أُنزِلَ مِنۢ بَعْدِ مُوسَىٰ
مُصَدِّقًا لِّمَا بَيْنَ يَدَيْهِ يَهْدِىٓ إِلَى ٱلْحَقِّ وَإِلَىٰ طَرِيقٍ مُّسْتَقِيمٍ
﴿٣٠﴾ يَٰقَوْمَنَآ أَجِيبُوا۟ دَاعِىَ ٱللَّهِ وَءَامِنُوا۟ بِهِۦ يَغْفِرْ لَكُم مِّن
ذُنُوبِكُمْ وَيُجِرْكُم مِّنْ عَذَابٍ أَلِيمٍ ﴿٣١﴾ وَمَن لَّا يُجِبْ دَاعِىَ ٱللَّهِ
فَلَيْسَ بِمُعْجِزٍ فِى ٱلْأَرْضِ وَلَيْسَ لَهُۥ مِن دُونِهِۦٓ أَوْلِيَآءُ ۚ أُو۟لَٰٓئِكَ
فِى ضَلَٰلٍ مُّبِينٍ ﴿٣٢﴾ أَوَلَمْ يَرَوْا۟ أَنَّ ٱللَّهَ ٱلَّذِى خَلَقَ ٱلسَّمَٰوَٰتِ
وَٱلْأَرْضَ وَلَمْ يَعْىَ بِخَلْقِهِنَّ بِقَٰدِرٍ عَلَىٰٓ أَن يُحْۦِىَ ٱلْمَوْتَىٰ ۚ بَلَىٰٓ
إِنَّهُۥ عَلَىٰ كُلِّ شَىْءٍ قَدِيرٌ ﴿٣٣﴾ وَيَوْمَ يُعْرَضُ ٱلَّذِينَ كَفَرُوا۟ عَلَى ٱلنَّارِ
أَلَيْسَ هَٰذَا بِٱلْحَقِّ ۖ قَالُوا۟ بَلَىٰ وَرَبِّنَا ۚ قَالَ فَذُوقُوا۟ ٱلْعَذَابَ بِمَا
كُنتُمْ تَكْفُرُونَ ﴿٣٤﴾ فَٱصْبِرْ كَمَا صَبَرَ أُو۟لُوا۟ ٱلْعَزْمِ مِنَ ٱلرُّسُلِ
وَلَا تَسْتَعْجِل لَّهُمْ ۚ كَأَنَّهُمْ يَوْمَ يَرَوْنَ مَا يُوعَدُونَ لَمْ يَلْبَثُوٓا۟ إِلَّا
سَاعَةً مِّن نَّهَارٍۭ ۚ بَلَٰغٌ ۚ فَهَلْ يُهْلَكُ إِلَّا ٱلْقَوْمُ ٱلْفَٰسِقُونَ ﴿٣٥﴾

## سُورَةُ مُحَمَّدٍ

آياتها ٣٨ — ترتيبها ٤٧

(29) **Ya kai wannan Manzo, ka ambaci lokacin da muka aika maka wata tawaga daga aljanu, suna sauraran Alqur'ani, wanda aka saukar maka, yayin da suka zo don sauraronsa, sai sashensu ya ce da sashe: "Ku yi shiru, don mu samu damar jin sa". Yayin Annabi (S.A.W) ya kammala karatunsa, sai aljanun suka koma ga mutanensu, suna yi musu gargaxi daga azabar Allah, idan ba su yi imani da wannan Alqur'ani ba.**

(30) **Sai suka ce musu: "Ya ku mutanenmu, haqiqa mu, mun ji wani littafi da Allah ya saukar bayan Annabi Musa, ya gasgata abin da ya gabace shi na littafan da aka saukar daga wajen Allah. Wannan littafi da muka saurara yana shiryarwa zuwa ga gaskiya da tafarki madaidaici, shi ne tafarkin musulunci".**

(31) **"Ya ku mutanen mu, ku amsa kiran Annabi Muhammad, cikin abin da ya kira ku zuwa gare shi na gaskiya, kuma yarda shi Manzo ne daga Ubangijinsa, sai Allah ya gafarta muku laifukanku, kuma ya kuvutar da ku daga azaba mai raxaxi, wadda take jiran ku idan baku amsa zuwa ga abin da yake kiran ku zuwa gare shi daga Ubangijinsa ba".**

(32) **Duk wanda bai amsawa Annabi Muhammad (S.A.W) cikin abin da yake kira zuwa gare shi na gaskiya ba. To ya sani ba zai tserewa Allah ba a bayan qasa, kuma ba shi da wasu mataimaka da za su tseratar da shi daga azaba koma bayan Allah, kuma waxannan su ne suke cikin vata bayyananne.**

(33) **Shin waxannan mushirikai, masu qaryatawa da tashi bayan mutuwa basu ga cewa: Allah da ya halicci sammai, kuma ya halicci qassai, kuma bai gaza a wurin halittar su ba, duk da girmansu da faxinsu, basu ga yana da ikon rayar da matattu ba, don yi musu hisabi da bada sakamako? Haka ne, tabbas shi mai iko ne a kan raya su, haqiqa shi (S.W.T) yana da iko a kan komai, ba zai gaza raya matattu ba.**

(34) **A ranar da za a bijiro da waxanda suka kafirce wa Allah da Manzanninsa ga wuta, don a azabtar da su a cikinta, kuma a ce musu: "Wannan abin da kuke gani na azaba ba gaskiya ne? Ko kuwa dai qarya ne, kamar yadda kuke faxa a duniya?! Sai su ce: "Gaskiya ne, mun rantse da Ubangijin mu, tabbas gaskiya ne". sai a ce musu: "Ku xanxani azaba, sakamakon kafircewar ku da Allah".**

(35) **Ya kai wannan Manzo, ka yi haquri a kan qaryatawar da mutanenka suke yi maka, irin haquri ma'abota azama daga Manzanni: Annabi Nuhu, da Ibrahim, da Musa, da Isa (S.A.W), kada ka gaggauto musu da azaba, kai ka ce masu qaryatawa daga cikin mutanenka ranar da zasu ga abin da ake alqawarta musu na azaba, basu tava zama a duniya ba sai wani xan lokaci a yini, saboda tsawon azabarsu. Wannan Alqur'ani, wanda aka saukarwa Annabi Muhammad (S.A.W) isarwa ne, kuma ya ishi mutum da aljan. Don haka ba a halakarwa da azaba sai mutanen da suka fita daga biyayya ga Allah, ta hanyar kafirci da savo.**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Yana daga ladabi mai kyau sauraron mai yin magana.**

**2 - Gaggawar amsa kiran da aljanun da suka shiriya suka yi, yana kwaxaitar da mutane su ma su aikata hakan.**

**3 - Amsa kiran gaskiya yana hukunta yin gaggawa wajen kira zuwa ga gaskiyar.**

**4 - Yin haquri xabi'a ce ta Annabawa.**

بِسْمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحْمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ وَصَدُّواْ عَن سَبِيلِ ٱللَّهِ أَضَلَّ أَعْمَٰلَهُمْ ١ وَٱلَّذِينَ
ءَامَنُواْ وَعَمِلُواْ ٱلصَّٰلِحَٰتِ وَءَامَنُواْ بِمَا نُزِّلَ عَلَىٰ مُحَمَّدٍ وَهُوَ ٱلْحَقُّ مِن
رَّبِّهِمْ كَفَّرَ عَنْهُمْ سَيِّـَٔاتِهِمْ وَأَصْلَحَ بَالَهُمْ ٢ ذَٰلِكَ بِأَنَّ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ
ٱتَّبَعُواْ ٱلْبَٰطِلَ وَأَنَّ ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ ٱتَّبَعُواْ ٱلْحَقَّ مِن رَّبِّهِمْ كَذَٰلِكَ يَضْرِبُ
ٱللَّهُ لِلنَّاسِ أَمْثَٰلَهُمْ ٣ فَإِذَا لَقِيتُمُ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ فَضَرْبَ ٱلرِّقَابِ حَتَّىٰٓ
إِذَآ أَثْخَنتُمُوهُمْ فَشُدُّواْ ٱلْوَثَاقَ فَإِمَّا مَنًّۢا بَعْدُ وَإِمَّا فِدَآءً حَتَّىٰ تَضَعَ ٱلْحَرْبُ
أَوْزَارَهَا ذَٰلِكَ وَلَوْ يَشَآءُ ٱللَّهُ لَٱنتَصَرَ مِنْهُمْ وَلَٰكِن لِّيَبْلُوَاْ بَعْضَكُم
بِبَعْضٍ وَٱلَّذِينَ قُتِلُواْ فِي سَبِيلِ ٱللَّهِ فَلَن يُضِلَّ أَعْمَٰلَهُمْ ٤ سَيَهْدِيهِمْ
وَيُصْلِحُ بَالَهُمْ ٥ وَيُدْخِلُهُمُ ٱلْجَنَّةَ عَرَّفَهَا لَهُمْ ٦ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ
ءَامَنُوٓاْ إِن تَنصُرُواْ ٱللَّهَ يَنصُرْكُمْ وَيُثَبِّتْ أَقْدَامَكُمْ ٧ وَٱلَّذِينَ كَفَرُواْ
فَتَعْسًا لَّهُمْ وَأَضَلَّ أَعْمَٰلَهُمْ ٨ ذَٰلِكَ بِأَنَّهُمْ كَرِهُواْ مَآ أَنزَلَ ٱللَّهُ
نصف الحزب ٥١ فَأَحْبَطَ أَعْمَٰلَهُمْ ٩ ۞ أَفَلَمْ يَسِيرُواْ فِي ٱلْأَرْضِ فَيَنظُرُواْ كَيْفَ كَانَ
عَٰقِبَةُ ٱلَّذِينَ مِن قَبْلِهِمْ دَمَّرَ ٱللَّهُ عَلَيْهِمْ وَلِلْكَٰفِرِينَ أَمْثَٰلُهَا ١٠ ذَٰلِكَ
بِأَنَّ ٱللَّهَ مَوْلَى ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَأَنَّ ٱلْكَٰفِرِينَ لَا مَوْلَىٰ لَهُمْ ١١



# Suratu Muhammad

An Saukar Da Ita A Madinah

## Daga Manufofin Surar:

**Zaburar da Muminai a kan yin jihadi da qarfafa su, tare da nuna raunin kafirai :**

## Tafsir:

**1 Waxanda suka kafircewa Allah, suka kawar da mutane daga addinin Allah, Allah ya vata ayyukansu. 2 Waxanda suka yi imani da Allah, kuma suka yi ayyuka nagari, suka yi imani da abin da Allah ya saukar wa Manzonsa Muhammad (S.A.W) – wanda shi ne gaskiya daga ubangijinsu – to Allah ya kankare musu munanan ayyukansu, ba zai kama su da laifin ba, kuma ya gyara musu al'amuransu na duniya da lahira. 3 Wancan sakamakon da aka ambata na vangarori guda biyu, an ambace shi ne don waxanda suka kafirce wa Allah sun bi vata ne, waxanda suka yi imani da Allah da Manzonsa kuwa sun bi gaskiya daga Ubangijinsu, don haka sai sakamakonsu ya bambanta, don ayyukansu sun bambanta, kamar yadda Allah ya bayyana hukuncinsa ga vangarorin guda biyu, vangaren muninai da vangaren kafirai, to haka ma Allah yake bugawa mutane misalansu, don a haxa kowane abin da ya kama da xan uwansa. 4 Ya ku Muminai, idan kuka haxu da mayaqa daga cikin waxanda suka kafirce, to ku doki wuyansu da takubban ku, ku ci gaba da yaqar su, har ku yawaita kisa a cikinsu, ku tunvuke qarfinsu. Idan kuka yawaita kisa a cikinsu, to ku tsananta xauri ga ribatattu, idan kun kama su, to kuna da zavi gwargwadon abin da maslaha ta nuna, ko dai ku yi baiwa ku sake su ba tare da kun karvi wani abu ba, ko kuma su fanshi kansu da dukiya ko wanin ta. Ku ci gaba da yaqarsu da kama su, har sai yaqi ya qare, ta hanyar musuluntar kafirai, ko qulla yarjejjeniyar zaman lafiya. Wancan abin da aka ambata na jarrabar Muminai da kafirai, da jujjuyawar kwanaki, da cin nasarar sashe a kan sashe, shi ne hukuncin Allah, kuma da Allah ya ga damar ya bada nasara a kan kafirai, ba tare da yaqi ba, da ya bada nasarar a kansu, sai dai ya shar'anta yin jihadi ne don ya gwada sashen ku da sashe, ya jarraba wanda zai yi yaqi a cikin Muminai da wanda ba zai yi ba, kuma ya jarrabi kafiri da mumini, idan ya kashe mumini sai ya shiga Aljannah, idan kuma mumini ya kashe shi sai ya shiga wuta. Waxanda aka kashe su a kan tafarkin Allah, Allah ba zai vata musu ayyukansu ba. 5 Kuma da sannu zai datar da su ga bin gaskiya, a cikin rayuwar su ta duniya, ya gyara musu al'amuransu. 6 Ya shigar da su Aljannah ranar alqiyama, wadda ya yi musu bayanin siffofinta a duniya suka gane ta, kuma yana sanar da su gidajensu da masaukansu a lahira. 7 Ya ku waxanda suka yi imani da Allah, kuma suka yi aiki da abin da ya shar'anta musu, idan kun taimakawa Allah ta hanyar taimakawa Annabin sa da addinin sa, da kuma yaqar kafirai, to Allah zai taimaka muku ta hanyar ya ba ku rinjaye a kansu, kuma ya tabbatar da dugadugan ku yayin da kuka haxu da su a wurin yaqi. 8 Waxanda suka kafirce wa Allah da Manzonsa sun yi asara, sun tave, kuma Allah ya vata ladan ayyukansu. 9 Wancan uqubar da ta afka musu saboda basa son abin da Allah ya saukar ne ga Manzonsa na Alqur'ani, da abin da yake cikinsa na kaxaita Allah, don haka sai Allah ya vata ayyukansu, suka yi asarar duniya da lahira. 10 Shin waxannan masu qaryatawa basu yi tafiya ba ne a bayan qasa? Su lura da qarshen waxanda suka qaryata a gabaninsu ba? Haqiqa qarshe ne mai raxaxi, Allah ya ruguza gidajensu a kansu, kuma ya halaka su, ya halakar da iyalansu da 'ya'yan su da dukiyoyin su. Irin waxannan uquba ta tabbata ga kafirai a kowane zamani da wuri. 11 Wancan sakamakon da aka ambata na vangarorin guda biyun, ya zama haka ne, don Allah mai taimakon Muminai ne, su kuwa kafirai basu da mataimaki.**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Yin fatafata da abokan gaba ta hanyar kisa hanya ce mafi kyau da danqwafar da su. 2 - Kyautatawa da karvar fansa da yin kisa da bautarwa, duk zavi ne a cikin musulunci, don yin mu'amala da ribataccen yaqi kafiri, ana xaukan abin da ya dace da maslaha. 3 - Girman matsayin yin shahada a tafarkin Allah. 4 - Taimakon Allah ga Muminai, sharaxin samunsa shi ne su taimaki addininsa.**

إِنَّ ٱللَّهَ يُدۡخِلُ ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَعَمِلُواْ ٱلصَّٰلِحَٰتِ جَنَّٰتٖ تَجۡرِي مِن
تَحۡتِهَا ٱلۡأَنۡهَٰرُۖ وَٱلَّذِينَ كَفَرُواْ يَتَمَتَّعُونَ وَيَأۡكُلُونَ كَمَا تَأۡكُلُ ٱلۡأَنۡعَٰمُ
وَٱلنَّارُ مَثۡوٗى لَّهُمۡ ١٢ وَكَأَيِّن مِّن قَرۡيَةٍ هِيَ أَشَدُّ قُوَّةٗ مِّن قَرۡيَتِكَ
ٱلَّتِيٓ أَخۡرَجَتۡكَ أَهۡلَكۡنَٰهُمۡ فَلَا نَاصِرَ لَهُمۡ ١٣ أَفَمَن كَانَ عَلَىٰ بَيِّنَةٖ مِّن
رَّبِّهِۦ كَمَن زُيِّنَ لَهُۥ سُوٓءُ عَمَلِهِۦ وَٱتَّبَعُوٓاْ أَهۡوَآءَهُم ١٤ مَّثَلُ ٱلۡجَنَّةِ ٱلَّتِي
وُعِدَ ٱلۡمُتَّقُونَۖ فِيهَآ أَنۡهَٰرٞ مِّن مَّآءٍ غَيۡرِ ءَاسِنٖ وَأَنۡهَٰرٞ مِّن لَّبَنٖ لَّمۡ يَتَغَيَّرۡ
طَعۡمُهُۥ وَأَنۡهَٰرٞ مِّنۡ خَمۡرٖ لَّذَّةٖ لِّلشَّٰرِبِينَ وَأَنۡهَٰرٞ مِّنۡ عَسَلٖ مُّصَفّٗىۖ وَلَهُمۡ
فِيهَا مِن كُلِّ ٱلثَّمَرَٰتِ وَمَغۡفِرَةٞ مِّن رَّبِّهِمۡۖ كَمَنۡ هُوَ خَٰلِدٞ فِي ٱلنَّارِ وَسُقُواْ
مَآءً حَمِيمٗا فَقَطَّعَ أَمۡعَآءَهُمۡ ١٥ وَمِنۡهُم مَّن يَسۡتَمِعُ إِلَيۡكَ حَتَّىٰٓ إِذَا
خَرَجُواْ مِنۡ عِندِكَ قَالُواْ لِلَّذِينَ أُوتُواْ ٱلۡعِلۡمَ مَاذَا قَالَ ءَانِفًاۚ أُوْلَٰٓئِكَ
ٱلَّذِينَ طَبَعَ ٱللَّهُ عَلَىٰ قُلُوبِهِمۡ وَٱتَّبَعُوٓاْ أَهۡوَآءَهُمۡ ١٦ وَٱلَّذِينَ ٱهۡتَدَوۡاْ
زَادَهُمۡ هُدٗى وَءَاتَىٰهُمۡ تَقۡوَىٰهُمۡ ١٧ فَهَلۡ يَنظُرُونَ إِلَّا ٱلسَّاعَةَ
أَن تَأۡتِيَهُم بَغۡتَةٗۖ فَقَدۡ جَآءَ أَشۡرَاطُهَاۚ فَأَنَّىٰ لَهُمۡ إِذَا جَآءَتۡهُمۡ
ذِكۡرَىٰهُمۡ ١٨ فَٱعۡلَمۡ أَنَّهُۥ لَآ إِلَٰهَ إِلَّا ٱللَّهُ وَٱسۡتَغۡفِرۡ لِذَنۢبِكَ
وَلِلۡمُؤۡمِنِينَ وَٱلۡمُؤۡمِنَٰتِۗ وَٱللَّهُ يَعۡلَمُ مُتَقَلَّبَكُمۡ وَمَثۡوَىٰكُمۡ ١٩



**(12) Haqiqa Allah zai shigar da waxanda suka yi imani da Allah, da Manzonsa, kuma suka aikata ayyuka nagari, zai shigar da su Ajannatai da qoramu suke gudana a qarqashin gine-ginenta da bishiyoyinta. Waxanda suka kafirce da Allah da Manzonsa suna jin daxi a duniya ta hanyar bin sha'awarsu, kuma suna ci kamar yadda dabbobi suke ci, ba su da wata damuwa sai cikinsu da farjinsu. Kuma wuta ce makomarsu da matabbatarsu ranar alqiyama, gare ta zasu koma.**

**(13) Alqaryu nawa ne daga cikin alqaryun al'ummun da suka gabata sun fi alqaryarka qarfi da yawan dukiya da 'ya'ya, sama da garin Makkah, wadda mutanenta suka fitar da kai daga cikinta, amma su ma mun halakar da su, yayin da suka qaryata Manzanninsu, kuma ba su samu wani mataimaki ba, da zai tseratar da su daga azabar Allah yayin da ta zo musu, don haka halakar da mutanen Makkah ba zai gagare mu ba idan muka yi nufi halakar da su.**

**(14) Shin wanda yake da hujja bayyananniya da dalili daga Ubangijinsa, yana bauta masa a kan basira, zai yi daidai da wanda Shaixan ya qawata masa mummunan aikinsa, kuma suka biyewa abin da soye-soyen zukatansu suka riya musu, na bautawa gumaka, da aikata laifuka, da qaryata Manzanni?.**

**(15) Siffar Aljannar da Allah ya yi alqawarinta ga masu tsoronsa, ta hanyar kamanta umarninsa, da nisantar abubuwan da ya hana, a cikinta akwai qoramu na ruwa, wadda qanshinsa ko xanxanonsa bai canza ba, saboda daxewa, kuma a cikinta akwai qoramu na nono wanda xanxanonsa bai canza ba, a cikinta akwai qoramu na giya mai daxi ga masu shan ta, da qoramu na zuma, wadda aka tace ta daga duk abin da zai iya vata ta, kuma suna da duk abin da suke so na kayan marmari, kuma qari a kan haka Allah zai shafe musu dukkan zunubansu, ba za a kama su da su ba, shin wanda wannan shi ne halinsa zai yi daidai da wanda sakamakonsa shi ne zama a cikin wuta, ba zai fita daga cikinta ba har abada, kuma za a shayar da shi ruwa mai tsananin zafi, ya yayyanke 'ya'yan hanjin cikinsu, saboda tsananin zafi?!.**

**(16) Ya kai wannan Manzo, akwai daga cikin munafukai wanda yake sauraran ka, sauraron da babu imani a cikinsa, sai dai bijirewa, idan kuma sun fito daga wurinka, sai su riqa tambayar ma'abota ilimi suna cewa: "Me ya faxa xazu a maganarsa?" suna nuna masu sani ba, sannan suna bijirewa. To waxannan su ne waxanda Allah ya rufe zukatansu, alheri baya isa gare ta, kuma suka bi son zukatansu, ya makantar da su daga gaskiya.**

**(17) Waxanda suka shiryu zuwa ga tafarkin gaskiya, da bin abin da Manzo ya zo da shi, Ubangijin su zai qara musu shiriya, da dacewa ga alheri, kuma ya kimsa musu yin aiki da abin da zai kare su daga faxawa cikin wuta.**

**(18) To shin kafirai suna jiran alqiyama ta zo musu ne babu tsammani?! to alamomin ta sun zo, daga ciki akwai aiko Manzon Allah (S.A.W) da tsagewar wata, to da yaya zasu tuna idan alqiyama ta zo musu?.**

**(19) Ya kai wannan Manzo ka sakankancewa babu wani abin bautawa ga gaskiya sai Allah, kuma ka nemi gafarar zunubanka a wurin Allah, kuma ka nemawa Muminai maza da mata gafarar zunubansu. Allah ya san abin da kuke aikatawa a cikin yinin ku, kuma ya san makwantar ku a cikin daren ku, babu wani abu cikin haka da yake vuya a gare shi.**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Taqaituwa damuwar kafirai a kan jin daxin Duniya kaxai, daxin da ba zai tabbata ba. 2 - Gwadawa tsakanin sakamakon muminai, da sakamakon kafirai, yana bayyana banbanci mai yawa a tsakaninsu, don mai hankali ya zavi zama mumini, shi kuma wawa ya zavi zama kafiri. 3 - Bayanin munana ladabin munafukai ga Annabi (S.A.W). 4 - Gabatar ilimi a kan magana da aiki.**

وَيَقُولُ ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ لَوۡلَا نُزِّلَتۡ سُورَةٞۖ فَإِذَآ أُنزِلَتۡ سُورَةٞ
مُّحۡكَمَةٞ وَذُكِرَ فِيهَا ٱلۡقِتَالُ رَأَيۡتَ ٱلَّذِينَ فِي قُلُوبِهِم مَّرَضٞ
يَنظُرُونَ إِلَيۡكَ نَظَرَ ٱلۡمَغۡشِيِّ عَلَيۡهِ مِنَ ٱلۡمَوۡتِۖ فَأَوۡلَىٰ لَهُمۡ
٢٠ طَاعَةٞ وَقَوۡلٞ مَّعۡرُوفٞۚ فَإِذَا عَزَمَ ٱلۡأَمۡرُ فَلَوۡ صَدَقُواْ ٱللَّهَ
لَكَانَ خَيۡرٗا لَّهُمۡ ٢١ فَهَلۡ عَسَيۡتُمۡ إِن تَوَلَّيۡتُمۡ أَن تُفۡسِدُواْ
فِي ٱلۡأَرۡضِ وَتُقَطِّعُوٓاْ أَرۡحَامَكُمۡ ٢٢ أُوْلَٰٓئِكَ ٱلَّذِينَ لَعَنَهُمُ
ٱللَّهُ فَأَصَمَّهُمۡ وَأَعۡمَىٰٓ أَبۡصَٰرَهُمۡ ٢٣ أَفَلَا يَتَدَبَّرُونَ ٱلۡقُرۡءَانَ
أَمۡ عَلَىٰ قُلُوبٍ أَقۡفَالُهَآ ٢٤ إِنَّ ٱلَّذِينَ ٱرۡتَدُّواْ عَلَىٰٓ أَدۡبَٰرِهِم
مِّنۢ بَعۡدِ مَا تَبَيَّنَ لَهُمُ ٱلۡهُدَى ٱلشَّيۡطَٰنُ سَوَّلَ لَهُمۡ وَأَمۡلَىٰ
لَهُمۡ ٢٥ ذَٰلِكَ بِأَنَّهُمۡ قَالُواْ لِلَّذِينَ كَرِهُواْ مَا نَزَّلَ ٱللَّهُ
سَنُطِيعُكُمۡ فِي بَعۡضِ ٱلۡأَمۡرِۖ وَٱللَّهُ يَعۡلَمُ إِسۡرَارَهُمۡ ٢٦
فَكَيۡفَ إِذَا تَوَفَّتۡهُمُ ٱلۡمَلَٰٓئِكَةُ يَضۡرِبُونَ وُجُوهَهُمۡ
وَأَدۡبَٰرَهُمۡ ٢٧ ذَٰلِكَ بِأَنَّهُمُ ٱتَّبَعُواْ مَآ أَسۡخَطَ ٱللَّهَ
وَكَرِهُواْ رِضۡوَٰنَهُۥ فَأَحۡبَطَ أَعۡمَٰلَهُمۡ ٢٨ أَمۡ حَسِبَ
ٱلَّذِينَ فِي قُلُوبِهِم مَّرَضٌ أَن لَّن يُخۡرِجَ ٱللَّهُ أَضۡغَٰنَهُمۡ ٢٩



**(20) Waxanda suka yi imani da Allah – suna burin Allah ya saukarwa Manzonsa wata sura, da zata qunshi hukunce hukuncen yaqi - suna cewa: "Ina ma Allah ya saukar da wata sura da zata ambaci yin yaqi". To idan Allah ya saukar da wata sura wadda a cikin bayaninta da hukunce-hukuncenta aka ambaci yaqi, sai ka ga waxanda a cikin zuciyarsu akwai shakka daga cikin munafukai suna kallonka, irin kallon wanda ya suma saboda tsananin tsoro da razana, don haka sai Allah ya yi musu alqawarin cewa azabarsu ta kusa, saboda qin su ga yaqi da kuma tsoronsa.**

**(21) Da zasu yi biyayya ga umarnin Allah, kuma su faxi magana mai kyau, wadda babu mummuna a cikinta, da ya fi musu alheri. kuma idan aka wajabta yin yaqi, tsanani ya yi tsanani, to da za su gasgata Allah cikin imaninsu da shi, da yi masa xa'a, da ya fi musu alheri, akan yin munafinci da sava umarnin Allah.**

**(22) Abin da ya bayyana daga halinku, idan kuka bijire daga imani da Allah, da yi masa xa'a, to zaku yi varna a bayan qasa, ta hanyar kafirci da savon Allah, kuma ku yanke zumunci, kamar yadda halinku ya kasance a lokacin Jahiliyya.**

**(23) Waxancan da suka siffantu da yin varna a bayan qasa, da yanke zumunci, su ne waxanda Allah ya nesanta su daga barin rahamarsa, kuma ya kurumtar da jin su, daga jin gaskiya, ji na karva da miqa wuya, ya kuma makantar da ganinsu, daga ganin gaskiya, na na xaukan izina.**

**(24) Ina ma waxannan masu bijirewar, sun bibiyi Alqur'ani, sun lura da abin da yake cikinsa?! Da sun bibiye shi, sun lura da shi, da ya nusantar da su zuwa ga dukkan alheri, ya nisantar da su daga dukkan sharri, ko kuwa a kan zukatan waxannan akwai murfi ne, wanda ya kulleta ruf, don haka wa'azi baya isa gare ta, kuma tunatarwa bata mata amfani?.**

**(25) Haqiqa waxanda suka yi ridda daga imaninsu zuwa kafirci da munafunci bayan hujja ta tsaya a gare su, gaskiya Annabi (S.A.W) ta bayyana gare su, shaixan ne kawai ya qawata musu kafurci da munafunci, ya kuma sauwaqe musu shi, ya ruxe su da dogon buri.**

**(26) Wannan vatarwar da ta same su, saboda sun faxa a voye, sun cewa mushirikai, waxanda basa son abin da Allah ya saukar ga Manzonsa na daga wahayi: "Zamu yi muku biyayya a cikin wasu al'amura, kamar kashe gwiwa a kan fita jihadi". To Allah ya san abin da suke voyewa, da abin da suke bayyanawa, babu abin da yake vuya a gare shi, don haka sai ya bayyana abin da ya ga dama ga Manzonsa (S.A.W).**

**(27) Yaya kake ganin irin halin da suke ciki na azaba da mummunan yanayi, idan Mala'ikun da aka wakilta su karvi rayukansu, suka karve su, suna dukan fuskokinsu da duburarsu da gudumu na qarfe.**

**(28) Waccan azabar, ta same su ne saboda sun biyewa duk abin da ya fusata Allah, na kafirci da munafunci, da savawa Allah da Manzonsa, kuma suka qi duk abin da zai kusantar da su ga Ubangijinsu, ya haifar musu da yardarsa, na daga imani da Allah, da bin Manzonsa, don haka sai Allah ya vata ayyukansu.**

**(29) Shin waxanda a cikin zukatansu akwai shakka daga cikin munafukai suna tsammanin Allah ba zai bayyana mugun nufinsu ya bankaxo asirin su ba?. Wallahi sai ya tona musu asiri, ta hanyar jarrabawa da musifu, domin mai imani na gaskiya ya bambanta da maqaryaci, kuma munini ya bayyana, munafuki kuma ya tozarta.**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Kallafa yin jihadi a tafarkin Allah, yana bambance munafukai daga sahun Muminai.**

**2 - Muhimmancin hankaltar littafin Allah, da haxarin ba shi baya da bijire masa.**

**3 - Yin varna a bayan qasa, da yanke zumunci, suna daga cikin sabubban da suka kawo qarancin dacewa da nisa daga rahamar Allah.**

وَلَوۡ نَشَآءُ لَأَرَيۡنَٰكَهُمۡ فَلَعَرَفۡتَهُم بِسِيمَٰهُمۡۚ وَلَتَعۡرِفَنَّهُمۡ فِي
لَحۡنِ ٱلۡقَوۡلِۚ وَٱللَّهُ يَعۡلَمُ أَعۡمَٰلَكُمۡ ٣٠ وَلَنَبۡلُوَنَّكُمۡ حَتَّىٰ نَعۡلَمَ
ٱلۡمُجَٰهِدِينَ مِنكُمۡ وَٱلصَّٰبِرِينَ وَنَبۡلُوَاْ أَخۡبَارَكُمۡ ٣١ إِنَّ ٱلَّذِينَ
كَفَرُواْ وَصَدُّواْ عَن سَبِيلِ ٱللَّهِ وَشَآقُّواْ ٱلرَّسُولَ مِنۢ بَعۡدِ
مَا تَبَيَّنَ لَهُمُ ٱلۡهُدَىٰ لَن يَضُرُّواْ ٱللَّهَ شَيۡـٔٗا وَسَيُحۡبِطُ أَعۡمَٰلَهُمۡ
ثلاثة أرباع الحزب ٥١ ٣٢ ۞ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُوٓاْ أَطِيعُواْ ٱللَّهَ وَأَطِيعُواْ ٱلرَّسُولَ
وَلَا تُبۡطِلُوٓاْ أَعۡمَٰلَكُمۡ ٣٣ إِنَّ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ وَصَدُّواْ عَن سَبِيلِ
ٱللَّهِ ثُمَّ مَاتُواْ وَهُمۡ كُفَّارٞ فَلَن يَغۡفِرَ ٱللَّهُ لَهُمۡ ٣٤ فَلَا تَهِنُواْ
وَتَدۡعُوٓاْ إِلَى ٱلسَّلۡمِ وَأَنتُمُ ٱلۡأَعۡلَوۡنَ وَٱللَّهُ مَعَكُمۡ وَلَن يَتِرَكُمۡ
أَعۡمَٰلَكُمۡ ٣٥ إِنَّمَا ٱلۡحَيَوٰةُ ٱلدُّنۡيَا لَعِبٞ وَلَهۡوٞۚ وَإِن تُؤۡمِنُواْ وَتَتَّقُواْ
يُؤۡتِكُمۡ أُجُورَكُمۡ وَلَا يَسۡـَٔلۡكُمۡ أَمۡوَٰلَكُمۡ ٣٦ إِن يَسۡـَٔلۡكُمُوهَا
فَيُحۡفِكُمۡ تَبۡخَلُواْ وَيُخۡرِجۡ أَضۡغَٰنَكُمۡ ٣٧ هَٰٓأَنتُمۡ هَٰٓؤُلَآءِ
تُدۡعَوۡنَ لِتُنفِقُواْ فِي سَبِيلِ ٱللَّهِ فَمِنكُم مَّن يَبۡخَلُۖ وَمَن يَبۡخَلۡ
فَإِنَّمَا يَبۡخَلُ عَن نَّفۡسِهِۦۚ وَٱللَّهُ ٱلۡغَنِيُّ وَأَنتُمُ ٱلۡفُقَرَآءُۚ وَإِن
تَتَوَلَّوۡاْ يَسۡتَبۡدِلۡ قَوۡمًا غَيۡرَكُمۡ ثُمَّ لَا يَكُونُوٓاْ أَمۡثَٰلَكُم ٣٨



**(30) Ya kai wannan Manzo, da mun ga dama sanar da kai munafukai da mun sanar da kai su, sai ka gane su da alamominsu, amma da sannu zaka gane su ta salon zancensu. Allah ne mafi sanin ayyukanku, babu abin da yake vuyar masa, kuma zai saka muka a kansu.**

**(31) Ya ku Muminai, Wallahi zamu jarrabe ku, ta hanyar jihadi da yaqar abokan gaba, da kisa, har mu bayyana masu jihadi a cikinku a kan tafarkin Allah, da masu yin haquri a kan yaqar maqiyan Allah, kuma zamu jarrabaku, domin mu bayyana mai gaskiya daga cikinku, da kuma maqaryaci.**

**(32) Haqiqa waxanda suka kafirce wa Allah da Manzonsa, kuma suka kange kawunansu daga addinin Allah, kuma suka kange wasunsu, suka savawa Manzonsa, suka yi qiyayya da shi, bayan ya bayyana shi Annabi ne, baza su cuci Allah da komai ba, kansu zasu cuta, kuma Allah zai vata ayyukansu.**

**(33) Ya ku waxanda suka yi imani da Allah, kuma suka yi aiki da abin da ya shar'anta, ku yi wa Allah xa'a, kuma ku yi wa Manzo xa'a, ta hanyar kamanta umarninsu, da nisantar haninsu, kada ku vata ayyukanku da yin kafirci da riya.**

**(34) Haqiqa waxanda suka kafirce wa Allah, kuma suka kawar da kawunansu, suka kawar da mutane daga barin addinin Allah, sannan suka mutu a kan kafircinsu, gabanin su tuba, to Allah ba zai gafarta musu laifukansu ba, ta hanyar rufa musu asiri, tabbas sai ya kama su da laifukansu, kuma ya shigar da su cikin wuta, suna masu dauwama a cikinta har abada.**

**(35) Ya ku Muminai kada ku yi rauni wurin tunkarar abokan gabarku, ku kira su zuwa ga sulhu tun gabanin su kira ku, alhali ku ne masu galaba da samun nasara a kansu. Allah yana tare da ku da nasararsa da qarfafawarsa, ba zai rage muku komai ba na daga ladan ayyukanku, kai, zai ma qara muku, saboda kyautarsa da falalarsa.**

**(36) Kaxai dai rayuwar duniya wasa ce da wargi, kada mai hankali ya shagala da ita ga barin yin aiki domin lahirarsa, kuma idan har kuka yi imani da Allah da Manzonsa, kuka ji tsoron Allah, ta hanyar kamanta umarninsa, da nisantar haninsa, tabbas zai baku ladan ayyukanku cikakke, ba tare da ragi ba, ba kuma zai nemi ku bashi dukiyarku gaba xaya ba, kaxai zai nemi ku bada abin da ya zama wajibi na daga zakka.**

**(37) Domin da a ce zai nemi ku bashi dukkanin dukiyarku, kuma ya ya matsa muku a kan haka, lallai zaku yi rowa, abin da yake cikin zukatanku na rashin son ciyarwa a tafarkin Allah ya bayyana, don haka ya bar tambayar duka dukiyarku don tausasawa a gare ku.**

**(38) Ga shi ku waxannan ana kiran ku ku ciyar da wani vangare na dukiyarku a tafarkin Allah, ba a neman ku ciyar da dukiyarku gaba xaya, amma a cikinku akwai wanda yake qin ciyar da abin da ake nema saboda rowa, to duk wanda ya yi rowar wani vangare na dukiyarsa a tafarkin Allah, to alal-haqiqa kansa ya yi wa, don ya hana kansa samun ladan ciyarwar, Allah shi ne cikakken mawadaci, baya buqatar ciyarwar ku, ku, ku ne cikakkun mabuqata gare shi, kuma idan kuka bar musulunci zuwa kafirci zai halakar da ku, ya zo da wasu mutanen ba ku ba, sannan baza su kasance kamarku ba, zasu kasance masu yi masa biyayya.**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Asiran munafukai da munanan abubuwan da suke zuciyarsu, suna bayyana a kan fuskokinsu, da salon maganganunsu.**

**2 - Jarrabawa sunna ce ta Allah, domin bambance muminai daga munafukai.**

**3 - Qarfafawar da Allah ga bayinsa Muminai, ta hanyar basu nasara, da datar da su.**

**4 - Yana daga cikin tausayawar Allah ga bayinsa bai nemi su ciyar da dukkan dukiyarsu ba.**

سُورَةُ الفَتْحِ
آيَاتُهَا ٢٩ — تَرْتِيبُهَا ٤٨

بِسۡمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحۡمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ
إِنَّا فَتَحۡنَا لَكَ فَتۡحٗا مُّبِينٗا ١ لِّيَغۡفِرَ لَكَ ٱللَّهُ مَا تَقَدَّمَ مِن ذَنۢبِكَ
وَمَا تَأَخَّرَ وَيُتِمَّ نِعۡمَتَهُۥ عَلَيۡكَ وَيَهۡدِيَكَ صِرَٰطٗا مُّسۡتَقِيمٗا ٢
وَيَنصُرَكَ ٱللَّهُ نَصۡرًا عَزِيزًا ٣ هُوَ ٱلَّذِيٓ أَنزَلَ ٱلسَّكِينَةَ فِي قُلُوبِ
ٱلۡمُؤۡمِنِينَ لِيَزۡدَادُوٓاْ إِيمَٰنٗا مَّعَ إِيمَٰنِهِمۡۗ وَلِلَّهِ جُنُودُ ٱلسَّمَٰوَٰتِ
وَٱلۡأَرۡضِۚ وَكَانَ ٱللَّهُ عَلِيمًا حَكِيمٗا ٤ لِّيُدۡخِلَ ٱلۡمُؤۡمِنِينَ وَٱلۡمُؤۡمِنَٰتِ
جَنَّٰتٖ تَجۡرِي مِن تَحۡتِهَا ٱلۡأَنۡهَٰرُ خَٰلِدِينَ فِيهَا وَيُكَفِّرَ عَنۡهُمۡ
سَيِّـَٔاتِهِمۡۚ وَكَانَ ذَٰلِكَ عِندَ ٱللَّهِ فَوۡزًا عَظِيمٗا ٥ وَيُعَذِّبَ
ٱلۡمُنَٰفِقِينَ وَٱلۡمُنَٰفِقَٰتِ وَٱلۡمُشۡرِكِينَ وَٱلۡمُشۡرِكَٰتِ ٱلظَّآنِّينَ
بِٱللَّهِ ظَنَّ ٱلسَّوۡءِۚ عَلَيۡهِمۡ دَآئِرَةُ ٱلسَّوۡءِۖ وَغَضِبَ ٱللَّهُ عَلَيۡهِمۡ
وَلَعَنَهُمۡ وَأَعَدَّ لَهُمۡ جَهَنَّمَۖ وَسَآءَتۡ مَصِيرٗا ٦ وَلِلَّهِ جُنُودُ
ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضِۚ وَكَانَ ٱللَّهُ عَزِيزًا حَكِيمًا ٧ إِنَّآ
أَرۡسَلۡنَٰكَ شَٰهِدٗا وَمُبَشِّرٗا وَنَذِيرٗا ٨ لِّتُؤۡمِنُواْ بِٱللَّهِ وَرَسُولِهِۦ
وَتُعَزِّرُوهُ وَتُوَقِّرُوهُۚ وَتُسَبِّحُوهُ بُكۡرَةٗ وَأَصِيلًا ٩



# Suratul Fathi

An Saukar Da Ita A Madinah

## Daga Manufofin Surar:

**Ambaton alqawarin Allah na samun buxi, da kafa Annabinsa da Muminai masu gaskiya a cikin taimakon addini a bayan qasa.**

## Tafsir:

**1 Haqiqa mun yi maka buxi - Ya kai wannan Manzo - buxi bayyananne da yin sulhun Hudaibiyya.**

**2 Domin Allah ya gafarta maka abin da ya gabata kafin wannan sulhun na laifukanka, da abin da ya yi jinkiri daga baya, kuma ya cika maka ni'imarsa a kanka, ta hanyar taimakon addininka, kuma ya shiryar da kai tafarki madaidaici, wanda babu karkata a cikinsa, shi ne tafarkin musulunci miqaqqe.**

**3 Kuma domin Allah ya taimake ka a kan maqiyanka, taimako mai qarfi, wanda babu mai tunkuxe shi.**

**4 Allah ne wanda ya saukar da tabbata da nutsuwa, a cikin zukatan Muminai, domin su qara imani a kan imaninsu. Rundunar da take cikin sammai da qassai mallakin Allah ce shi kaxai, yana qarfafa wanda ya ga dama daga cikin bayinsa da ita. Haqiqa Allah Masani ne ga masalahar bayinsa, kuma mai hikima ne cikin abin da yake gudanarwa na taimako da qarfafawa.**

**5 Domin Allah ya shigar da waxanda suka yi imani da Allah da Manzonsa maza da mata cikin Aljannatai, da qoramu ke gudana ta qarqashin gidajensu da bishiyoyinsu, kuma ya shafe musu laifukansu, ba zai kama su da su ba. Wannan abin da aka ambata, na samun abin da ake nema, shi ne Aljannah, da nisanta daga abin da ake tsoro, shi ne kama mutum da munanan ayyukansa – wannan abin a wurin Allah rabo ne mai girma, babu rabon da kai shi.**

**6 Kuma ya azabtar da munafukai maza da mata, da mushirikai maza da mata, masu zaton Allah ba zai taimaki addininsa ba, kuma ba zai xaukaka kalmar sa ba, amma sai azaba ta afka musu, Allah ya yi fushi da su, saboda kafircinsu, da mummunan zatonsu, kuma ya kore su daga rahamarsa, ya tanadar musu wutar jahannama a lahira, zasu shige ta, su dauwama a cikinta har abada. Makomar da za su koma gare ta, wutar Jahannama ta yi muni.**

**7 Rundunar da take cikin sammai da qassai mallakar Allah ce, yana qarfafa wanda ya ga dama daga cikin bayinsa da ita. Haqiqa Allah ya tabbata Mabuwayi, babu wanda yake rinjayarsa, kuma mai hikima ne a cikin halittarsa, da qaddarawarsa, da gudanarwarsa.**

**8 Ya kai wannan Manzo, haqiqa mun aiko ka a matsayin mai shaida ga al'ummarka ranar alqiyama, kuma mai yin bushara ga Muminai da abin da Allah ya tanadar musu na taimako da kafuwa, da abin da ya tanadar musu a lahira na daga ni'imomi, kuma kana tsoratar da kafirai da abin da Allah ya tanadar musu a duniya na qasqanci da karyewa a wajen yaqi a hannun muminai, da abin da ya tanadar musu a lahira na azaba mai raxaxi, wadda take jiransu.**

**9 Da fatan zaku yi imani da Allah, ku yi imani da Manzonsa, kuma ku girmama Manzonsa ku xaukaka shi, kuma ku ku tsarkake Allah a farkon yini da kuma qarshensa.**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Sulhun hudaibiya shi ne farkon buxi mai girma ga musulunci da musulmai. 2 - Nutsuwa alama ce daga cikin alamomin imani, wadda take kawo kwanciyar hankali da tabbata a kan abin da ake kai. 3 - Haxarin munanawa Allah zato, saboda Allah yana yi wa mutane mu'amala ne gwargwadon yadda suke yi masa zato. 4 - Wajabcin girmama manzon Allah da xaukaka shi (S.A.W).**

إِنَّ ٱلَّذِينَ يُبَايِعُونَكَ إِنَّمَا يُبَايِعُونَ ٱللَّهَ يَدُ ٱللَّهِ فَوْقَ
أَيْدِيهِمْ ۚ فَمَن نَّكَثَ فَإِنَّمَا يَنكُثُ عَلَىٰ نَفْسِهِۦ ۖ وَمَنْ أَوْفَىٰ
بِمَا عَٰهَدَ عَلَيْهُ ٱللَّهَ فَسَيُؤْتِيهِ أَجْرًا عَظِيمًا ١٠ سَيَقُولُ
لَكَ ٱلْمُخَلَّفُونَ مِنَ ٱلْأَعْرَابِ شَغَلَتْنَآ أَمْوَٰلُنَا وَأَهْلُونَا
فَٱسْتَغْفِرْ لَنَا ۚ يَقُولُونَ بِأَلْسِنَتِهِم مَّا لَيْسَ فِى قُلُوبِهِمْ ۚ قُلْ
فَمَن يَمْلِكُ لَكُم مِّنَ ٱللَّهِ شَيْـًٔا إِنْ أَرَادَ بِكُمْ ضَرًّا أَوْ أَرَادَ بِكُمْ
نَفْعًۢا ۚ بَلْ كَانَ ٱللَّهُ بِمَا تَعْمَلُونَ خَبِيرًۢا ١١ بَلْ ظَنَنتُمْ أَن لَّن
يَنقَلِبَ ٱلرَّسُولُ وَٱلْمُؤْمِنُونَ إِلَىٰٓ أَهْلِيهِمْ أَبَدًا وَزُيِّنَ ذَٰلِكَ فِى
قُلُوبِكُمْ وَظَنَنتُمْ ظَنَّ ٱلسَّوْءِ وَكُنتُمْ قَوْمًۢا بُورًا ١٢ وَمَن لَّمْ يُؤْمِنۢ
بِٱللَّهِ وَرَسُولِهِۦ فَإِنَّآ أَعْتَدْنَا لِلْكَٰفِرِينَ سَعِيرًا ١٣ وَلِلَّهِ مُلْكُ
ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضِ ۚ يَغْفِرُ لِمَن يَشَآءُ وَيُعَذِّبُ مَن يَشَآءُ ۚ
وَكَانَ ٱللَّهُ غَفُورًا رَّحِيمًا ١٤ سَيَقُولُ ٱلْمُخَلَّفُونَ إِذَا
ٱنطَلَقْتُمْ إِلَىٰ مَغَانِمَ لِتَأْخُذُوهَا ذَرُونَا نَتَّبِعْكُمْ ۖ يُرِيدُونَ
أَن يُبَدِّلُوا۟ كَلَٰمَ ٱللَّهِ ۚ قُل لَّن تَتَّبِعُونَا كَذَٰلِكُمْ قَالَ ٱللَّهُ مِن قَبْلُ ۖ
فَسَيَقُولُونَ بَلْ تَحْسُدُونَنَا ۚ بَلْ كَانُوا۟ لَا يَفْقَهُونَ إِلَّا قَلِيلًا ١٥



**(10) Haqiqa waxanda suke yi maka caffa - Ya kai wannan Manzo – caffar da ake kira (Bai'atur Ridwan), caffa ce a kan yaqar mushirikai mutanen Makkah, to kaxai dai waxannan suna yi wa Allah ne caffa, domin shi ne ya umarce su da yaqar mushirikai, kuma shi ne zai saka musu, hannun Allah yana saman hannayensu a yayin da suke yin wannan caffa, yana ganin su, babu wani abu nasu da yake vuya a gare shi. Don haka duk wanda ya warware caffarsa, bai cika alqawarin da ya yi wa Allah ba, na taimakon addininsa, to ya sani cutar warware caffarsa da warware alqawarinsa zai dawo a kansa ne, hakan ba zai cuci Allah da komai ba, wanda kuwa ya cika alqawarin da ya yi wa Allah na taimakon addininsa, to da sannu Allah zai ba shi lada mai girma, shi ne Aljannah.**

**(11) Ya kai wannan Manzo, waxanda Allah ya bar su a baya, wajen tafiya tare da kai zuwa Makkah daga cikin larabawan qauye, idan ka zarge su a kan rashin bin ka za su ce: "Kulawa da dukiyar mu, da 'ya'yanmu sun shagaltar da mu daga tafiya tare da kai, don haka ka nema mana gafarar zunubanmu a wurin Allah. Suna faxi da bakinsu abin da baya cikin zukatansu, na neman istigfarin Annabi (S.A.W) domin basu tuba daga laifukansu ba, to ka ce da su: "Babu wanda yake mallakar komai a wurin Allah a kanku, idan ya nufe ku da alheri, ko kuma ya nufe ku da sharri. Haqiqa Allah ya tabbata dangane da abin da kuke aikatawa masani ne mai bada labari, babu wani abin da yake vuyar masa a cikin ayyukan, duk irin yadda kuka voye su.**

**(12) Kuma abin da kuka ba da uzuri da shi, na kulawa da dukiya, da 'ya'ya, ba shi ne ya hana ku tafiya tare da shi ba, kawai dai kuna zaton Annabi (S.A.W) da sahabbansa za su halaka ne gaba xaya, ba za su dawo wurin iyalansu a garin Madina ba, kuma Shaixan ne ya qawata muku haka a cikin zukatanku. kuma kuka yi mummunan zato ga Ubangijinku cewa: ba zai taimaki Annabinsa ba. Don haka kun kasance halakakku, saboda abin da kuka yi na munana zato ga Allah, da qin tafiya tare da Manzon sa.**

**(13) Duk wanda bai yi imani da Allah, da Manzon sa ba, to shi kafiri ne, kuma haqiqa mun tanadi wuta mai ci ganga-ganga ga kafirai a ranar tashin alqiyama, wadda za a yi musu azaba a cikinta.**

**(14) Na Allah ne kaxai mulkin sammai da qassai, yana gafarta zunuban wanda ya ga dama daga cikin bayinsa, ya shigar da shi Aljannah da falalarsa, kuma yana azabtar da wanda ya ga dama daga cikin bayinsa, bisa adalcinsa. Allah ya tabbata mai yawan gafara ga zunuban wanda ya tuba daga cikin bayinsa, kuma mai jin tausayin su.**

**(15) Waxanda Allah bai basu damar zuwa jihadi ba, za su cewa Muminai idan kuka tafi zuwa ganimar khaibar, wadda Allah ya yi muku alqawarin ta, bayan kammaluwar sulhun Hudaibiya don ku xauko ta: "Ku bari mu tafi tare da ku ko ma samo daga ganimar". Waxannan da basu je yaqin ba suna son su canza alqawarin da Allah ya yi wa Muminai bayan sulhun Hudaibiya na zai basu ganimar Khaibar su kaxai. To ka ce da su - Ya kai wannan Manzo -: "ba zaku bi mu zuwa ga wannan ganimar ba, saboda Allah ya yi mana alqawari ganimar khaibar ta waxanda suka halarci sulhun Hudaibiyya ne kaxai". Za su ce: "Hana mu bin ku zuwa khaibar ba umarnin Allah ba ne, kawai dai hassada kuke yi mana". Amma kuma lamarin ba kamar yadda waxannan waxanda ba su je yaqi suke zato ba ne, kawai su basa fahimtar umarni da hanin Allah ne, sai 'yan kaxan, don haka suka faxa cikin sava masa.**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Matsayin (Bai'atur Ridwan) a wurin Allah yana da girma, kuma ma'abotanta suna cikin mafi alherin mutane a bayan qasa. 2 - Munanawa Allah zato yana cikin dalilan faxawa cikin savon Allah, yana iya kaiwa ma zuwa ga kafirci. 3 - Masu raunin imani 'yan kaxan ne yayin da aka shiga tsoro, amma suna da yawa a wajen kwaxayin abin duniya.**

قُل لِّلۡمُخَلَّفِينَ مِنَ ٱلۡأَعۡرَابِ سَتُدۡعَوۡنَ إِلَىٰ قَوۡمٍ أُوْلِي بَأۡسٖ شَدِيدٖ
تُقَٰتِلُونَهُمۡ أَوۡ يُسۡلِمُونَۖ فَإِن تُطِيعُواْ يُؤۡتِكُمُ ٱللَّهُ أَجۡرًا حَسَنٗاۖ
وَإِن تَتَوَلَّوۡاْ كَمَا تَوَلَّيۡتُم مِّن قَبۡلُ يُعَذِّبۡكُمۡ عَذَابًا أَلِيمٗا ١٦ لَّيۡسَ
عَلَى ٱلۡأَعۡمَىٰ حَرَجٞ وَلَا عَلَى ٱلۡأَعۡرَجِ حَرَجٞ وَلَا عَلَى ٱلۡمَرِيضِ حَرَجٞۗ
وَمَن يُطِعِ ٱللَّهَ وَرَسُولَهُۥ يُدۡخِلۡهُ جَنَّٰتٖ تَجۡرِي مِن تَحۡتِهَا
الحزب ٥٢ ٱلۡأَنۡهَٰرُۖ وَمَن يَتَوَلَّ يُعَذِّبۡهُ عَذَابًا أَلِيمٗا ١٧ ۞ لَّقَدۡ رَضِيَ ٱللَّهُ
عَنِ ٱلۡمُؤۡمِنِينَ إِذۡ يُبَايِعُونَكَ تَحۡتَ ٱلشَّجَرَةِ فَعَلِمَ مَا فِي
قُلُوبِهِمۡ فَأَنزَلَ ٱلسَّكِينَةَ عَلَيۡهِمۡ وَأَثَٰبَهُمۡ فَتۡحٗا قَرِيبٗا ١٨ وَمَغَانِمَ
كَثِيرَةٗ يَأۡخُذُونَهَاۗ وَكَانَ ٱللَّهُ عَزِيزًا حَكِيمٗا ١٩ وَعَدَكُمُ ٱللَّهُ
مَغَانِمَ كَثِيرَةٗ تَأۡخُذُونَهَا فَعَجَّلَ لَكُمۡ هَٰذِهِۦ وَكَفَّ أَيۡدِيَ
ٱلنَّاسِ عَنكُمۡ وَلِتَكُونَ ءَايَةٗ لِّلۡمُؤۡمِنِينَ وَيَهۡدِيَكُمۡ صِرَٰطٗا
مُّسۡتَقِيمٗا ٢٠ وَأُخۡرَىٰ لَمۡ تَقۡدِرُواْ عَلَيۡهَا قَدۡ أَحَاطَ ٱللَّهُ بِهَاۚ
وَكَانَ ٱللَّهُ عَلَىٰ كُلِّ شَيۡءٖ قَدِيرٗا ٢١ وَلَوۡ قَٰتَلَكُمُ ٱلَّذِينَ
كَفَرُواْ لَوَلَّوُاْ ٱلۡأَدۡبَٰرَ ثُمَّ لَا يَجِدُونَ وَلِيّٗا وَلَا نَصِيرٗا ٢٢ سُنَّةَ
ٱللَّهِ ٱلَّتِي قَدۡ خَلَتۡ مِن قَبۡلُۖ وَلَن تَجِدَ لِسُنَّةِ ٱللَّهِ تَبۡدِيلٗا ٢٣



**16 Ya kai wannan Manzo, ka faxawa waxanda suka qi tafiya tare da kai zuwa Makkah, daga cikin mutanen qauye, kana mai basu labari: "Za a kirawo ku zuwa ga yaqar wasu mutane masu tsanani, da qarfi a wajen yaqi, zaku yaqe su saboda Allah, ko su shiga musulunci, ba tare da an yi yaqi ba, idan kuka yi wa Allah xa'a cikin wannan kira da ya yi muku na yaqar su, to zai baku lada mai kyau, shi ne Aljannah, idan kuwa kuka bada baya ga barin yi masa xa'a, kamar yadda kuka bada baya ga barin fita tare da Manzon Allah zuwa Makkah, zai azabtar da ku azaba mai ciwo".**

**17 Wanda aka yi masa uzuri domin makanta, ko gurgunta, ko rashin lafiya, ba shi da wani laifi idan bai fita yaqi saboda Allah ba, Duk wanda ya yi xa'a ga Allah, ya yi xa'a ga Manzonsa zai shigar da shi Aljannah, wadda qoramu ke gudana ta qarqashin gidajensu da bishiyoyinsu, wanda kuwa ya bijire ga barin yi musu xa'a, zai azabtar da shi azaba mai ciwo.**

**18 Tabbas Allah ya yarda da Muminai, a lokacin da suke yi maka caffa a Hudaibiyya (Bai'atur Ridwan) a qarqashin bishiya, sai ya san abin da yake cikin zukatansu na imani, da tsarkin zuciya, da gaskiya, sai ya saukar da nutsuwa a cikin zukatansu, kuma ya saka musu a kan haka da buxi na kurkusa, shi ne buxe garin Khaibar, don ya canja musu a kan abin da suka rasa na shiga Makkah.**

**19 Kuma ya ba su ganima mai yawa, da suka samu daga mutanen khaibar, haqiqa Allah ya tabbata Mabuwayi, babu wanda yake rinjayarsa, kuma mai hikima a cikin halittarsa, da tsarawarsa da gudanarwarsa.**

**20 Ya ku Muminai Allah ya yi muku alqawarin wasu ganimomi masu yawa, waxanda zaku samu a yaqe yaqen Musulunci a nan gaba, amma sai ya gaggauto muku da ganimar khaibar, kuma ya hana hannun Yahudawa daga su afkawa iyalanku a bayanku, kuma don wannan ganimar da aka gaggauto muku ta zama wata alama ce gare ku, da take tabbatar da samun nasarar ku daga Allah, da qarfafawarsa a gare ku, kuma Allah yana shiryar da ku tafarki madaidaici, wanda babu karkata a cikinsa.**

**21 Kuma Allah ya yi muku alqawarin wasu ganimomin, waxanda baku iya samun su ba a wannan lokaci, Allah ne kaxai mai iko a kansu, kuma suna cikin iliminsa da kulawarsa, haqiqa Allah mai iko ne a kan komai, babu abin da yake gajiyar da shi.**

**22 Ya ku muminai da a ce: waxanda suka kafirce wa Allah da Manzonsa za su yaqe ku, da sun juya da gudu suna masu karaya a gaban ku, sannan ba za su samu wani majivincin lamari, da zai jivince su ba, kuma ba zasu samu wani mataimaki, da zai taimaka musu su a kan yaqin ku ba.**

**23 Samun galabar Muminai, da rugujewar kafirai, tabbatacciya ce a kowane zamani da kowane lokaci, sunnar Allah ce da ta gabata a cikin al'ummun da suka wuce, kafin waxannan masu qaryatawar, kuma ba zaka samu canji ba ga tsarin Allah - Ya kai wannan Manzo - .**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Labarun da Alqur'ani yake bayarwa na voyayyun abubuwa, waxanda duk sun tabbata daga baya, kamar buxe garuruwan Musulunci, to wannan dalili ne a kan Alqur'ani daga Allah yake.**
**2 - Hukunce-hukuncen shari'a sun ginu ne a kan sauki da tausasawa.**
**3 - Sakamakon waxanda suka halarci caffar (Bai'atur Ridwan) ya kasu biyu, akwai wanda aka gaggauta musu shi, akwai kuma wanda aka jinkirtar musu da shi sai a Lahira.**
**4 - Rinjayen gaskiya da ma'abotanta a kan vata, da ma'abotansa, sunna ce ta Allah.**

وَهُوَ ٱلَّذِي كَفَّ أَيۡدِيَهُمۡ عَنكُمۡ وَأَيۡدِيَكُمۡ عَنۡهُم بِبَطۡنِ مَكَّةَ مِنۢ
بَعۡدِ أَنۡ أَظۡفَرَكُمۡ عَلَيۡهِمۡۚ وَكَانَ ٱللَّهُ بِمَا تَعۡمَلُونَ بَصِيرًا ٢٤
هُمُ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ وَصَدُّوكُمۡ عَنِ ٱلۡمَسۡجِدِ ٱلۡحَرَامِ
وَٱلۡهَدۡيَ مَعۡكُوفًا أَن يَبۡلُغَ مَحِلَّهُۥۚ وَلَوۡلَا رِجَالٞ مُّؤۡمِنُونَ وَنِسَآءٞ
مُّؤۡمِنَٰتٞ لَّمۡ تَعۡلَمُوهُمۡ أَن تَطَـُٔوهُمۡ فَتُصِيبَكُم مِّنۡهُم مَّعَرَّةُۢ
بِغَيۡرِ عِلۡمٖۖ لِّيُدۡخِلَ ٱللَّهُ فِي رَحۡمَتِهِۦ مَن يَشَآءُۚ لَوۡ تَزَيَّلُواْ لَعَذَّبۡنَا
ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ مِنۡهُمۡ عَذَابًا أَلِيمًا ٢٥ إِذۡ جَعَلَ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ
فِي قُلُوبِهِمُ ٱلۡحَمِيَّةَ حَمِيَّةَ ٱلۡجَٰهِلِيَّةِ فَأَنزَلَ ٱللَّهُ سَكِينَتَهُۥ
عَلَىٰ رَسُولِهِۦ وَعَلَى ٱلۡمُؤۡمِنِينَ وَأَلۡزَمَهُمۡ كَلِمَةَ ٱلتَّقۡوَىٰ
وَكَانُوٓاْ أَحَقَّ بِهَا وَأَهۡلَهَاۚ وَكَانَ ٱللَّهُ بِكُلِّ شَيۡءٍ عَلِيمٗا ٢٦
لَّقَدۡ صَدَقَ ٱللَّهُ رَسُولَهُ ٱلرُّءۡيَا بِٱلۡحَقِّۖ لَتَدۡخُلُنَّ ٱلۡمَسۡجِدَ
ٱلۡحَرَامَ إِن شَآءَ ٱللَّهُ ءَامِنِينَ مُحَلِّقِينَ رُءُوسَكُمۡ وَمُقَصِّرِينَ
لَا تَخَافُونَۖ فَعَلِمَ مَا لَمۡ تَعۡلَمُواْ فَجَعَلَ مِن دُونِ ذَٰلِكَ
فَتۡحٗا قَرِيبًا ٢٧ هُوَ ٱلَّذِيٓ أَرۡسَلَ رَسُولَهُۥ بِٱلۡهُدَىٰ وَدِينِ
ٱلۡحَقِّ لِيُظۡهِرَهُۥ عَلَى ٱلدِّينِ كُلِّهِۦۚ وَكَفَىٰ بِٱللَّهِ شَهِيدٗا ٢٨



**(24) Allah shi ne wanda ya kame hannun mushirikai a kanku, lokacin da kusan mutum tamanin daga cikinsu suka zo, suna son cutar da ku a lokacin sulhun Hudaibiyya, kuma su ma ya kame hannunku daga gare su, ba ku kashe su ba, ba ku cutar da su ba, sai ma kuka sake su bayan kun samu damar kama su. Haqiqa Allah danagane da abin da kuke aikatawa mai gani ne, babu wani abu daga yake vuya a gare shi daga ayyukanku.**

**(25) Su ne waxanda suka kafirce wa Allah da Manzonsa, suka hana ku isa ga masallaci mai alfarma, kuma suka hana hadaya, suka tsare ta, suka hana ta isa Harami, wurin da za a yanka ta. Ba don samun wasu Muminai maza da mata ba, waxanda ba ku san su ba, kuma kada ya zamo kun kashe su tare da kafirai, kisan nasu ya sa ku yi laifi, ku biya diyya, alhali ba ku sani ba, da Allah ya yi muku izinin ku buxe Makkah, don Allah ya shigar da wanda ya ga dama cikin rahamarsa, kamar muminai da suke ciki Makkah. Da a ce kafirai sun ware daga Muminai a Makkah, da mun azabtar da waxanda suka kafirce wa Allah da Manzonsa azaba mai raxaxi.**

**(26) A lokacin da waxanda suka kafirce wa Allah da Manzonsa suka sanya girman kai, girman kai irin na Jahiliyya a cikin zukatansu, girman kan da bai da alaqa da tabbatar da gaskiya, sai dai kawai son zuciya, suka qyamaci shigar Manzon Allah (S.A.W) garin Makkah, a shekarar Hudaibiyya, don gudun kada a aibata su a ce ya samu galaba a kansu, to sai Allah ya saukar da nutsuwa ga Manzonsa, ya kuma saukar da ita ga Muminai, don haka fushi bai saka su sun fuskanci mushirikai da irin da abin da suke yi musu ba, kuma Allah ya lazimta wa Muminai riqo da kalmar gaskiya, ita ce La ilaha illal Lahu, kuma su tsaya da haqqinta, sai suka aikata hakan. Muminai sun kasance sun fi kowa cancanta da wannan kalma daga waninsu, kuma su ne ahalin ta, saboda abin da Allah ya sani na alheri a cikin zukatansu. Haqiqa Allah masani ne a kan dukkan komai, babu abin da yake vuya a gare shi.**

**(27) Haqiqa Allah ya tabbatarwa Manzonsa mafarkinsa da gaskiya, a yayin da ya nuna masa wannan mafarkin a cikin barcinsa, shi ne: Manzon Allah (S.A.W) da sahabbansa suna shiga xakin Allah mai alfarma, cikin aminci daga abokan gabarsu, wasu daga cikinsu sun aske kawunansu, wasu kuma sun yi saisaye, alamar aikin hajji ya qare. (Wannan shi ne mafarkin) Allah ya san maslaharku – Ya ku Muminai – abin da ku baku sani ba, don haka ya sanya rashin tabbatar wannan mafarki, na rashin shiga Makka a wannan shekara ya zama buxi na kusa, shi ne abin da Allah ya gudanar da shi na sulhun Hudaibiyya da abin da ya biyo bayan haka na buxe khaibar a hannun muminai, waxanda suka halacci sulhun Hudaibiyya.**

**(28) Allah shi ne wanda ya aiko da Manzonsa Muhammad (S.A.W) da bayani bayyananne, da addinin gaskiya, wanda shi ne addinin Musulunci, domin ya xaukaka shi a kan dukkan addinai, waxanda suka sava masa gaba xaya, kuma haqiqa Allah ya shaida da hakan, Allah kuma ya isa shaida a kan komai.**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Hana tafarkin Allah yaxuwa laifi ne, ma'abotansa sun cancanci azaba mai raxaxi.**

**2 - Abin da Allah yake tsarawa don maslahar bayinsa ya wuce sanin bayin.**

**3 - Tsoratarwa a kan canza 'yan uwantakar addini, da ta qabilanci ko Jahiliyya.**

**4 - Xaukakar addinin Musulunci sunnar Allah ce, kuma alqwarin Allah ya tabbata.**

مُّحَمَّدٌ رَّسُولُ ٱللَّهِ وَٱلَّذِينَ مَعَهُۥٓ أَشِدَّآءُ عَلَى ٱلْكُفَّارِ رُحَمَآءُ بَيْنَهُمْ
تَرَىٰهُمْ رُكَّعًا سُجَّدًا يَبْتَغُونَ فَضْلًا مِّنَ ٱللَّهِ وَرِضْوَٰنًا سِيمَاهُمْ
فِى وُجُوهِهِم مِّنْ أَثَرِ ٱلسُّجُودِ ذَٰلِكَ مَثَلُهُمْ فِى ٱلتَّوْرَىٰةِ وَمَثَلُهُمْ فِى
ٱلْإِنجِيلِ كَزَرْعٍ أَخْرَجَ شَطْـَٔهُۥ فَـَٔازَرَهُۥ فَٱسْتَغْلَظَ فَٱسْتَوَىٰ
عَلَىٰ سُوقِهِۦ يُعْجِبُ ٱلزُّرَّاعَ لِيَغِيظَ بِهِمُ ٱلْكُفَّارَ وَعَدَ ٱللَّهُ ٱلَّذِينَ
ءَامَنُوا۟ وَعَمِلُوا۟ ٱلصَّٰلِحَٰتِ مِنْهُم مَّغْفِرَةً وَأَجْرًا عَظِيمًۢا ﴿٢٩﴾

سُورَةُ الحُجُرَاتِ — آيَاتُهَا ١٨ — تَرْتِيبُهَا ٤٩

بِسْمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحْمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

الحِزْبُ ٥٢ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ لَا تُقَدِّمُوا۟ بَيْنَ يَدَىِ ٱللَّهِ وَرَسُولِهِۦ وَٱتَّقُوا۟
ٱللَّهَ إِنَّ ٱللَّهَ سَمِيعٌ عَلِيمٌ ﴿١﴾ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ لَا تَرْفَعُوٓا۟
أَصْوَٰتَكُمْ فَوْقَ صَوْتِ ٱلنَّبِىِّ وَلَا تَجْهَرُوا۟ لَهُۥ بِٱلْقَوْلِ كَجَهْرِ بَعْضِكُمْ
لِبَعْضٍ أَن تَحْبَطَ أَعْمَٰلُكُمْ وَأَنتُمْ لَا تَشْعُرُونَ ﴿٢﴾ إِنَّ ٱلَّذِينَ
يَغُضُّونَ أَصْوَٰتَهُمْ عِندَ رَسُولِ ٱللَّهِ أُو۟لَٰٓئِكَ ٱلَّذِينَ ٱمْتَحَنَ
ٱللَّهُ قُلُوبَهُمْ لِلتَّقْوَىٰ لَهُم مَّغْفِرَةٌ وَأَجْرٌ عَظِيمٌ ﴿٣﴾ إِنَّ ٱلَّذِينَ
يُنَادُونَكَ مِن وَرَآءِ ٱلْحُجُرَٰتِ أَكْثَرُهُمْ لَا يَعْقِلُونَ ﴿٤﴾



**(29) Muhammad (S.A.W) Manzon Allah ne. Sahabbansa dake tare da shi, masu tsanani ne ga kafiran da suke yaqar su, amma masu tausasawa ne da jinqai da soyayya a tsakaninsu. Zaka gan su – Ya kai mai duba - masu yawaita ruku'i, masu yawan sujjada ga Allah Maxaukakin sarki, suna neman Allah ya yi musu baiwar gafara da lada mai girma, kuma ya yarda da su. Alamarsu tana cikin fuskokinsu, daga guraben sujjada, shi ne abin da yake bayyana a gare su na shiriya, da hasken sallah a fuskokinsu. Wannan ita ce siffarsu da Attaura littafin da aka saukar wa Annabi Musa (A.S) ya siffata su da ita, amma misalinsu a cikin littafin Injila da aka saukar wa Annabi Isa (A.S) shi ne: su a wurin taimakon junansu, da kamalarsu, kamar shuka ce ta fitar da 'yan qarama, sai ta yi qarfi, ta yi kauri, ta daidaita a kan itacenta, qarfinta da cikarta yana birge manoma, (Allah ya sa sahabbai a haka ne) don ya baqantawa kafirai rai da abin da suke gani a tare da su na qarfi da haxuwa da cika. Alqawarin Allah ga wanda suka yi imani da Allah, suka yi ayyuka nagartattu daga cikin sahabbai shi gafara ga zunubansu, ba za a kama su da su ba, da kuma wani lada mai girma a wurin Allah, shi ne Aljannah.**

# Suratul Hujurat

An Saukar Da Ita A Madinah

## Daga Manufofin Surar:

**Bayanin xabi'u da halayen al'ummar Musulmi cikin zamantakewarsu, da tsoratarwa a kan munanan xabi'u.**

## Tafsir:

**(1) Ya ku waxanda suka yi imani da Allah, suka yi biyayya ga abin da ya shar'anta, kada ku shige gaba ga Allah da Manzonsa, da magana ko aiki. Ku ji tsoron Allah ta hanyar kamanta umarninsa, da nesantar abubuwan da ya hana, haqiqa Allah mai jin maganganin ku ne, kuma masani ne ga ayyukanku, babu abin da yake kuvuce masa daga cikinsu, kuma zai saka muka a kan ayyukanku.**

**(2) Ya ku waxanda suka yi imani da Allah, kuma suka yi biyayya ga abin da ya shar'anta, ku zamo masu ladabi tare da Manzonsa, kada ku sanya muryoyinku suna sama da muryar Annabi (S.A.W) yayin da kuke yi masa magana, kuma kada ku bayyana sunan shi, kamar yadda sashenku yake kiran sashe, ku kira shi da siffar Annabci ko Manzo, cikin magana mai taushi, don gudun kada ladan ayyukanku ya lalace da yin hakan, alhali baku san ladan yana vacewa ba.**

**(3) Haqiqa waxanda suke sassauta muryarsu a wurin Manzon Allah (S.A.W) waxannan su ne waxanda Allah ya jarrabi zukatansu da tsoronsa, ya kuma tace zuciyarsu don wannan, suna da gafarar zunubansu, baza a kama su da su ba, kuma suna da lada mai girma a ranar alqiyama, shi ne ya shigar da su Aljannah.**

**(4) Haqiqa waxanda suke kiranka - Ya kai wannan Manzo - daga cikin mutanen qauye, ta bayan xakunan matanka, da yawan su basu da hankali.**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - An shar'anta tausasawa mumini, da tsanantawa kafiri mai yaqar musulmi.**
**2 - Haxin kai da taimakekkeniya suna daga cikin halayyar sahabban Manzon Allah (S.A.W).**
**3 - Duk wanda yake jin haushin Sahabbai masu girma a zuciyarsa, ana ji masa tsoron faxawa cikin kafirci.**
**4 - Wajabcin yin ladabi tare da Manzon Allah (S.A.W), da sunnarsa, da kuma magadansa ( wato malamai).**

وَلَوۡ أَنَّهُمۡ صَبَرُواْ حَتَّىٰ تَخۡرُجَ إِلَيۡهِمۡ لَكَانَ خَيۡرٗا لَّهُمۡۚ وَٱللَّهُ غَفُورٞ
رَّحِيمٞ ٥ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُوٓاْ إِن جَآءَكُمۡ فَاسِقُۢ بِنَبَإٖ فَتَبَيَّنُوٓاْ أَن
تُصِيبُواْ قَوۡمَۢا بِجَهَٰلَةٖ فَتُصۡبِحُواْ عَلَىٰ مَا فَعَلۡتُمۡ نَٰدِمِينَ ٦
وَٱعۡلَمُوٓاْ أَنَّ فِيكُمۡ رَسُولَ ٱللَّهِۚ لَوۡ يُطِيعُكُمۡ فِي كَثِيرٖ مِّنَ ٱلۡأَمۡرِ لَعَنِتُّمۡ
وَلَٰكِنَّ ٱللَّهَ حَبَّبَ إِلَيۡكُمُ ٱلۡإِيمَٰنَ وَزَيَّنَهُۥ فِي قُلُوبِكُمۡ وَكَرَّهَ
إِلَيۡكُمُ ٱلۡكُفۡرَ وَٱلۡفُسُوقَ وَٱلۡعِصۡيَانَۚ أُوْلَٰٓئِكَ هُمُ ٱلرَّٰشِدُونَ ٧
فَضۡلٗا مِّنَ ٱللَّهِ وَنِعۡمَةٗۚ وَٱللَّهُ عَلِيمٌ حَكِيمٞ ٨ وَإِن طَآئِفَتَانِ
مِنَ ٱلۡمُؤۡمِنِينَ ٱقۡتَتَلُواْ فَأَصۡلِحُواْ بَيۡنَهُمَاۖ فَإِنۢ بَغَتۡ إِحۡدَىٰهُمَا
عَلَى ٱلۡأُخۡرَىٰ فَقَٰتِلُواْ ٱلَّتِي تَبۡغِي حَتَّىٰ تَفِيٓءَ إِلَىٰٓ أَمۡرِ ٱللَّهِۚ فَإِن فَآءَتۡ
فَأَصۡلِحُواْ بَيۡنَهُمَا بِٱلۡعَدۡلِ وَأَقۡسِطُوٓاْۖ إِنَّ ٱللَّهَ يُحِبُّ ٱلۡمُقۡسِطِينَ
٩ إِنَّمَا ٱلۡمُؤۡمِنُونَ إِخۡوَةٞ فَأَصۡلِحُواْ بَيۡنَ أَخَوَيۡكُمۡۚ وَٱتَّقُواْ ٱللَّهَ
لَعَلَّكُمۡ تُرۡحَمُونَ ١٠ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ لَا يَسۡخَرۡ قَوۡمٞ مِّن قَوۡمٍ
عَسَىٰٓ أَن يَكُونُواْ خَيۡرٗا مِّنۡهُمۡ وَلَا نِسَآءٞ مِّن نِّسَآءٍ عَسَىٰٓ أَن يَكُنَّ خَيۡرٗا
مِّنۡهُنَّۖ وَلَا تَلۡمِزُوٓاْ أَنفُسَكُمۡ وَلَا تَنَابَزُواْ بِٱلۡأَلۡقَٰبِۖ بِئۡسَ ٱلِٱسۡمُ
ٱلۡفُسُوقُ بَعۡدَ ٱلۡإِيمَٰنِۚ وَمَن لَّمۡ يَتُبۡ فَأُوْلَٰٓئِكَ هُمُ ٱلظَّٰلِمُونَ ١١



**(5) Kuma da ace waxannan masu kiran naka ta bayan xakunan matanka - Ya kai wannan Manzo - sun yi haquri basu kirawo ka ba, har sai da ka fito zuwa gare su, sannan su yi maka magana cikin sassauta murya, da hakan ya fiye musu alheri a kan su riqa kiranka ta baya, saboda abin da yake cikin haka na girmamawa gare ka, amma Allah mai yawan gafara ne ga zunuban wanda ya tuba daga cikinsu, da wasun su ma, mai gafarta musu ne saboda jahilcinsu, kuma mai jin qan su ne.**
**(6) Ya ku waxanda suka yi imani da Allah, kuma suka yi aiki da abin da ya shar'anta, idan fasiqi ya zo muku da wani labari na wasu mutane, to ku tabbatar da ingancin labarinsa, kada ku yi gaggawar gasgata shi, don gudun kada in kun gasgata labarinsa, ba tare da bincike ba, ku afkawa wasu mutane, alhali baku da masaniyar haqiqanin al'amarinsu, sai ku wayi gari bayan kun afka musu kuna yin nadama, yayin da qaryar labarinsa ta bayyana gare ku. (7) Ku sani cewa – Ya ku muminai - a cikinku akwai Manzon Allah, a wahayi yana sauka a gare shi, don haka ku kiyayi yin qarya, sai wahayi ya sauka ya bada labarin qaryarku, Allah shi ne mafi sanin abin da zai amfane ku, da zai biye muku cikin da yawa daga abin da kuke bada shawara a kai, da kun faxa cikin wahalar da baya son ku faxa cikinta, sai dai Allah saboda falalarsa a gare ku ya saka muku son imani, ya qawata shi a cikin zukatanku, sai kuka yi imani, kuma ya sanya muku qin kafirci, da qin yi masa xa'a, da sava masa. Waxanda suka siffatu da abin da aka faxa tabbas su ne masu bin tafarkin shiriya da kuma daidai. (8) Kuma duk abin da ya same ku, na qawata alheri a cikin zukatan ku, da qin sharri, duk daga falalar Allah ne, da ya yi muku ita, kuma ni'ima ce da ya yi muku ita. Haqiqa Allah masani ne da wanda ya gode masa cikin bayinsa, don haka sai ya datar da shi, kuma mai hikima ne, ta yadda yake ajiye komai a inda ya dace. (9) Idan vangare guda biyu na Muminai suka yi faxa, ko yaqi, to ku daidaita tsakaninsu – Ya ku Muminai - ta hanyar kiransu zuwa ga hukunta shari'ar Allah a cikin wannan faxan nasu. Idan wani vangare daga cikinsu ya qi yarda da sulhun, kuma ya yi ta'addanci, to ku yaqi xan ta'addan har sai ya komo zuwa ga hukuncin Allah, idan ya komo zuwa ga hukuncin Allah, to ku yi sulhu a tsakaninsu da adalci, ku yi adalci a cikin hukuncinku a tsakaninsu. Haqiqa Allah yana son masu yin adalci a cikin hukuncinsu. (10) Kaxai dai Muminai 'yan uwan juna ne a Musulunci, ita kuwa 'yan uwantaka ta Musulunci, tana koya ku yi sulhu – Ya ku Muminai – a tsakanin yan uwanku masu savani. ku ji tsoron Allah ta hanyar kamanta umarninsa, da nisantar abubuwan da ya hana, ko kwa samu rahama. (11) Ya ku waxanda suka yi imani da Allah, kuma suka yi aiki da abin da ya shar'anta, kada wasu mutane daga cikinku su riqa yin izgili ga wasu mutane, domin ta yiwu waxanda ake yi musu izgilin sun fi alheri a wurin Allah, kuma ana izina ne da abin da yake wurin Allah. Kada mata su yi wa mata izgili, don zata iya yiwuwa waxanda ake yi wa izgilin sun fi alheri a wurin Allah. Kada ku aibata 'yan uwanku, domin kamar kanku kuka aibata. Kada sashenku ya aibata sashe da wani laqabi da basa so, kamar yadda wasu mutanen Madinah suka kasance suna yi kafin zuwan Manzon Allah (S.A.W). Duk wanda ya aikata haka daga cikinku to ya zama fasiqi, tir da sifar fasiqanci bayan imani, kuma duk wanda bai tuba daga waxannan laifuka ba, to waxannan su ne waxanda suka zalunci kansu, ta hanyar kai kansu zuwa ga halaka, saboda abin da suke aikatawa na savo.**

**Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa: 1 - Wajabcin bincike a kan ingancin labarai, Musamman labaran da wanda ake tuhuma da kafirci yake kawo wa. 2 - Wajabcin yin sulhu tsakanin musulman da suke faxa da juna, da kuma halaccin yaqar vangaren da ya zarce a kan yin ta'addanci, da qin yin sulhu. 3 - Yana daga cikin haqqin 'yan uwantakar imani: yin sulhu tsakanin masu rigima da juna, da nisantar duk abin da zai vatawa juna rai, na izgili, da aibantawa, da jifan juna da laqabin da basa so.**

يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ ٱجۡتَنِبُواْ كَثِيرٗا مِّنَ ٱلظَّنِّ إِنَّ بَعۡضَ ٱلظَّنِّ
إِثۡمٞۖ وَلَا تَجَسَّسُواْ وَلَا يَغۡتَب بَّعۡضُكُم بَعۡضًاۚ أَيُحِبُّ أَحَدُكُمۡ أَن
يَأۡكُلَ لَحۡمَ أَخِيهِ مَيۡتٗا فَكَرِهۡتُمُوهُۚ وَٱتَّقُواْ ٱللَّهَۚ إِنَّ ٱللَّهَ
تَوَّابٞ رَّحِيمٞ ١٢ يَٰٓأَيُّهَا ٱلنَّاسُ إِنَّا خَلَقۡنَٰكُم مِّن ذَكَرٖ وَأُنثَىٰ وَجَعَلۡنَٰكُمۡ
شُعُوبٗا وَقَبَآئِلَ لِتَعَارَفُوٓاْۚ إِنَّ أَكۡرَمَكُمۡ عِندَ ٱللَّهِ أَتۡقَىٰكُمۡۚ إِنَّ ٱللَّهَ
عَلِيمٌ خَبِيرٞ ١٣ ۞قَالَتِ ٱلۡأَعۡرَابُ ءَامَنَّاۖ قُل لَّمۡ تُؤۡمِنُواْ وَلَٰكِن نصف الحزب ٥٢
قُولُوٓاْ أَسۡلَمۡنَا وَلَمَّا يَدۡخُلِ ٱلۡإِيمَٰنُ فِي قُلُوبِكُمۡۖ وَإِن تُطِيعُواْ ٱللَّهَ
وَرَسُولَهُۥ لَا يَلِتۡكُم مِّنۡ أَعۡمَٰلِكُمۡ شَيۡـًٔاۚ إِنَّ ٱللَّهَ غَفُورٞ رَّحِيمٌ ١٤
إِنَّمَا ٱلۡمُؤۡمِنُونَ ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ بِٱللَّهِ وَرَسُولِهِۦ ثُمَّ لَمۡ يَرۡتَابُواْ
وَجَٰهَدُواْ بِأَمۡوَٰلِهِمۡ وَأَنفُسِهِمۡ فِي سَبِيلِ ٱللَّهِۚ أُوْلَٰٓئِكَ هُمُ
ٱلصَّٰدِقُونَ ١٥ قُلۡ أَتُعَلِّمُونَ ٱللَّهَ بِدِينِكُمۡ وَٱللَّهُ يَعۡلَمُ مَا فِي
ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَمَا فِي ٱلۡأَرۡضِۚ وَٱللَّهُ بِكُلِّ شَيۡءٍ عَلِيمٞ ١٦ يَمُنُّونَ
عَلَيۡكَ أَنۡ أَسۡلَمُواْۖ قُل لَّا تَمُنُّواْ عَلَيَّ إِسۡلَٰمَكُمۖ بَلِ ٱللَّهُ يَمُنُّ
عَلَيۡكُمۡ أَنۡ هَدَىٰكُمۡ لِلۡإِيمَٰنِ إِن كُنتُمۡ صَٰدِقِينَ ١٧ إِنَّ ٱللَّهَ يَعۡلَمُ
غَيۡبَ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضِۚ وَٱللَّهُ بَصِيرُۢ بِمَا تَعۡمَلُونَ ١٨



**(12) Ya ku waxanda suka yi imani da Allah, kuma suka yi aiki da abin da ya shar'anta, ku nisanci da yawa daga cikin tuhume tuhume, waxanda basu da madogara, ko wasu dalilai da alamomi da zasu sa a yi su, haqiqa wani vangaren na zato laifi ne, kamar mummunan zato ga wanda a zahirinsa nagari ne. Kada ku bibiyi al'aurar Muminai, kada xayanku ya ambaci xan uwansa da abin da baya so, domin ambatonsa da abin da baya so kamar cin namansa ne bayan ya mutu, yanzu xayanku zai so ya ci naman xan uwansa a mace?. Don haka ku qyamaci yin gulmarsa don daidai take da hakan. Ku ji tsoron Allah ta hanyar kamanta umarninsa, da kuma nisantar haninsa. Haqiqa Allah mai yawan karvar tuba ne ga duk wanda ya tuba daga cikin bayinsa, kuma mai jin qai ne a gare su.**

**(13) Ya ku mutane, haqiqa mun halicce ku daga namiji guda, shi ne babanku Adam, da kuma mace guda, ita ce babarku Hauwa'u, don haka nasabar ku xaya ce, kada sashenku ya yi alfahari ga sashe a wajen dangantaka, kuma mun sanya ku bayan haka ku zama mutane da yawa, kuma qabilu waxanda suka yaxu, domin sashenku ya san sashe, ba don sashe ya yi alfahari a kan sashe ba, don ba a samun bambance da fifiko sai da tsoron Allah, don haka ma Allah ya ce: Mafi girmanku a wurin Allah shi ne wanda ya fi ku tsoronsa. Haqiqa Allah masanin halinku ne, kuma masani ne mai bada labari da halin da kuke ciki na cika ko tawaya, babu abin da yake vuya a gare shi.**

**(14) Wasu daga cikin mutanen qauye suka ce, yayin da suka zo wajen Annabi (S.A.W): "Mun yi imani da Allah da Manzonsa". To ka faxa musu ya kai wannan Manzo: "Baku yi imani ba, kawai dai ku ce mun musulunta, mun miqa wuya, har yanzu imani bai shiga zukatanku ba tukun, amma ana san ran zai shiga. Idan kuka yi wa Allah da Manzonsa biyayya, ta hanyar imani da aiki nagari, da nisantar haramun, to Allah ba zai rage muku komai da ladan ayyukanku ba. Haqiqa Allah mai yawan gafara ne ga wanda ya tuba daga cikin bayinsa, kuma mai jin qan su ne.**

**(15) Haqiqa Muminai su ne waxanda suka yi imani da Allah da Manzonsa, sannan babu wata shakka da ta haxu da imaninsu, kuma suka yi jihadi da dukiyoyinsu da rayukansu a tafarkin Allah, sannan basu yi rowar wani abu ba. Waxannan da suka siffantu da waxannan siffofi su ne masu gaskiya a cikin imaninsu.**

**(16) Ya kai wannan Manzo, ka faxawa waxannan mutanen qauye: "Shin kuna sanar da Allah ne, kuna nuna masa addininku?!. Alhali Allah ya san duk abin da yake cikin sammai, kuma ya san duk abin da yake cikin qassa. Allah ya san dukkan komai, babu abin da yake vuyar masa, don haka baya buqatar ku sanar da shi addininku, ko ku nuna masa. (17) Ya kai wannan Manzo, mutanen qauye suna yi maka gori a kan cewa sun musulunta. Ka ce da su: "kada ku yi min gorin shigar ku addinin Allah, domin amfanin hakan idan ya tabbata gare ku zai koma, kuma gaskiya ma Allah ne ya kamata ya yi muku gori, saboda datar da ku da ya yi ga yin imani da shi, idan har da gaske kuke yi a cikin da'awarku cewa kun shiga cikin addinin.**

**(18) Haqiqa Allah ya san duk abin da ya vuya a cikin sammai, kuma ya san duk abin da ya vuya a cikin qasa, babu abin da yake vuyar masa daga ciki, kuma Allah mai gani ne ga ayyukanku, babu wani abin da yake vuya a gare shi daga ayyukanku, kuma da sannu zai saka muku a kansu, masu kyau da marasa kyau.**

**Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:** **1 - Munanawa mutanen kirki zato laifi ne, kuma ya halatta a yi taka-tsantsan daga mutanen banza, ta hanyar munana musu zato. 2 - Kasancewar tushen 'yan adam xaya ne, hakan yana wajabta a watsar da duk wani alfahari da nasaba. 3 - Imani ba faxa da baki ba ne ba tare da qudirin zuci ba, a'a shi imani qudircewa ne a zuciya, da faxi da baki, da aiki da gavvai. 4 - Datarwa ga shirya a hannun Allah kaxai take, kuma falala ce daga Allah, ba haqqin wani ba ne da dole a ba shi kayansa.**

# Suratu Qaaf

An Saukar Da Ita A Makkah



سُورَةُ قٓ — آيَاتُهَا ٤٥ — تَرۡتِيبُهَا ٥٠

بِسۡمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحۡمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

قٓۚ وَٱلۡقُرۡءَانِ ٱلۡمَجِيدِ ١ بَلۡ عَجِبُوٓاْ أَن جَآءَهُم مُّنذِرٞ مِّنۡهُمۡ
فَقَالَ ٱلۡكَٰفِرُونَ هَٰذَا شَيۡءٌ عَجِيبٌ ٢ أَءِذَا مِتۡنَا وَكُنَّا تُرَابٗاۖ ذَٰلِكَ
رَجۡعُۢ بَعِيدٞ ٣ قَدۡ عَلِمۡنَا مَا تَنقُصُ ٱلۡأَرۡضُ مِنۡهُمۡۖ وَعِندَنَا كِتَٰبٌ
حَفِيظُۢ ٤ بَلۡ كَذَّبُواْ بِٱلۡحَقِّ لَمَّا جَآءَهُمۡ فَهُمۡ فِيٓ أَمۡرٖ مَّرِيجٍ ٥
أَفَلَمۡ يَنظُرُوٓاْ إِلَى ٱلسَّمَآءِ فَوۡقَهُمۡ كَيۡفَ بَنَيۡنَٰهَا وَزَيَّنَّٰهَا
وَمَا لَهَا مِن فُرُوجٖ ٦ وَٱلۡأَرۡضَ مَدَدۡنَٰهَا وَأَلۡقَيۡنَا فِيهَا رَوَٰسِيَ
وَأَنۢبَتۡنَا فِيهَا مِن كُلِّ زَوۡجِۭ بَهِيجٖ ٧ تَبۡصِرَةٗ وَذِكۡرَىٰ لِكُلِّ عَبۡدٖ
مُّنِيبٖ ٨ وَنَزَّلۡنَا مِنَ ٱلسَّمَآءِ مَآءٗ مُّبَٰرَكٗا فَأَنۢبَتۡنَا بِهِۦ جَنَّٰتٖ
وَحَبَّ ٱلۡحَصِيدِ ٩ وَٱلنَّخۡلَ بَاسِقَٰتٖ لَّهَا طَلۡعٞ نَّضِيدٞ ١٠ رِّزۡقٗا
لِّلۡعِبَادِۖ وَأَحۡيَيۡنَا بِهِۦ بَلۡدَةٗ مَّيۡتٗاۚ كَذَٰلِكَ ٱلۡخُرُوجُ ١١ كَذَّبَتۡ قَبۡلَهُمۡ
قَوۡمُ نُوحٖ وَأَصۡحَٰبُ ٱلرَّسِّ وَثَمُودُ ١٢ وَعَادٞ وَفِرۡعَوۡنُ وَإِخۡوَٰنُ
لُوطٖ ١٣ وَأَصۡحَٰبُ ٱلۡأَيۡكَةِ وَقَوۡمُ تُبَّعٖۚ كُلّٞ كَذَّبَ ٱلرُّسُلَ فَحَقَّ وَعِيدِ
١٤ أَفَعَيِينَا بِٱلۡخَلۡقِ ٱلۡأَوَّلِۚ بَلۡ هُمۡ فِي لَبۡسٖ مِّنۡ خَلۡقٖ جَدِيدٖ ١٥



## Daga cikin manufofin surar:

**Farkar da rafkanannun zukata kan haqiqanin yadda tashi bayan mutuwa yake, da bada sakamako ranar alqiyama, da kawo hujjoji a kan hakan, da bayanin abubuwan da zasu faru.**

## Tafsir:

**(1) (Qaaf) Bayani a kan ire-iren waxannan haruffa ya gabata a farkon suratul Baqarah. Allah ya rantse da Alqur'ani mai girma, saboda abin da ya qunsa na ma'anoni da alherai da albarka, cewa: lallai za a tashe ku ranar alqiyama, domin yi muku hisabi da bada sakamako. (2) Kafirai sun qi karvar Alqur'ani ba don tunanin qarya ka yi musu ba, domin sun san gaskiyarka, kawai dai suna mamaki ne a ce Manzo ya zo musu daga jinsin su, ba daga cikin Mala'iku ba, suka ce saboda mamaki da suke yi: "Zuwan Manzo daga cikin jinsin mutane zuwa gare mu yana da ban mamaki"!. (3) Yanzu za a tashe mu bayan mun mutu, mun zama turvaya? Wannan tashi da kuma dawowar rayuwar ga jikkunan mu bayan sun ruve ba abu ne ba mai yiwuwa ba, ba zai tava faruwa ba. (4) Tabbas mun san abin da qasa take ci daga jikinsu, bayan mutuwarsu da qarewar rayuwarsu, babu wani abin da ya vuyar mana daga ciki, kuma a wurin mu akwai littafi mai kiyaye duk abin da Allah ya tsara musu a cikin rayuwarsu da kuma bayan mutuwarsu.**

**(5) Kawai dai waxannan mushirikai sun qaryata Alqur'ani ne, yayin da Manzo ya zo musu da shi, don haka suna cikin ruxani, basa tabbata a kan abu xaya. Yayin da Allah ya ambaci inkarin da mushirikai suke yi a kan tashi bayan mutuwa, sai ya tunatar da su dalilan da suke nuna faruwar haka, ya ce:**

**(6) Waxannan masu qaryata ranar tashi bayan mutuwa ba su yi la'akari da sama ba, ta yadda muka halicce ta, muka gina ta, muka qawata da abin da muka sanya a cikinta na taurari, kuma bata da wasu qofofi da za su aibata ta. To wanda ya halicci wannan saman ba zai gaza tashin mamata a raye ba. (7) Qasa kuma mun shimfixa ta, daidai da yadda za a iya zama a kanta, kuma muka sanya duwatsu tabbatattu a cikinta, don kada ta riqa motsawa, kuma muka fitar da tsirrai da bishiyoyi masu ban sha'awa da kyan gani. (8) Mun halicci duk wannan ne, don ya zama abin lura da tunatarwa ga dukkan wani bawa mai komawa zuwa ga Ubangijisa da yi masa biyayya. (9) Mun saukar da ruwa daga sama mai yawan amfani da alheri, sai muka tsiro da gonaki da wannan ruwan, muka tsirar da abin da kuke girbewa na kwayar abinci da waninsa. (10) Kuma muka tsiro da bishiyoyin dabino dogwaye, waxanda suke da furanni masu yawa, wasu kan wasu. (11) Mun fitar da abin da muka fitar don arziki ga bayi, da za su ci gare shi, kuma muka raya wani gari matacce, wanda babu tsiro a cikinsa da shi. Kamar yadda muka raya wannan gari matacce da wannan ruwan, haka muke raya matattu, sai su fito daga makwancinsu suna rayayyu.**

**(12) Kafin waxannan masu qaryatawar da kai – Ya kai wannan Manzo – wasu mutane sun qaryata Annabawansu. Mutanen Annabi Nuhu da mutanen garin rijiya sun qaryata, Samudawa ma sun qaryata. (13) Adawa ma sun qaryata, haka ma Fir'auna da mutanen Annabi Luxu. (14) Mutanen Annabi Shu'aibu sun qaryata shi, da mutanen garin Tubba'i sarkin Yemen, don haka sai abin da Allah ya yi musu alqawari na azaba ya tabbata a kansu**

**(15) Shin mun gaza halittar ku ne a karon farko, ballantana mu gaza tashin ku bayan mutuwa? Kawai dai suna cikin ruxu ne a kan sake sabuwar halitta bayan halittarsu ta farko.**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Mushirikai suna ganin Aannabta ta yi wa jinsin mutum girma, amma kuma suna bawa duwatsu siffar allantaka!. 2 - Da halittar Sammai, da halittar qassai, da saukar da ruwan sama, da tsirar da busasshiyar qasa, da halittar mutane a karon farko, dukkansu hujjoji ne da dalilai masu tabbatar da yiwuwar tashin alqiyama. 3 - Qaryata Manzanni al'ada ce ta al'ummun da suka gabata, kuma yin uquba ga masu qaryatawa sunnar Allah ce.**

وَلَقَدۡ خَلَقۡنَا ٱلۡإِنسَٰنَ وَنَعۡلَمُ مَا تُوَسۡوِسُ بِهِۦ نَفۡسُهُۥۖ وَنَحۡنُ أَقۡرَبُ إِلَيۡهِ
مِنۡ حَبۡلِ ٱلۡوَرِيدِ ١٦ إِذۡ يَتَلَقَّى ٱلۡمُتَلَقِّيَانِ عَنِ ٱلۡيَمِينِ وَعَنِ ٱلشِّمَالِ
قَعِيدٞ ١٧ مَّا يَلۡفِظُ مِن قَوۡلٍ إِلَّا لَدَيۡهِ رَقِيبٌ عَتِيدٞ ١٨ وَجَآءَتۡ سَكۡرَةُ
ٱلۡمَوۡتِ بِٱلۡحَقِّۖ ذَٰلِكَ مَا كُنتَ مِنۡهُ تَحِيدُ ١٩ وَنُفِخَ فِي ٱلصُّورِۚ ذَٰلِكَ
يَوۡمُ ٱلۡوَعِيدِ ٢٠ وَجَآءَتۡ كُلُّ نَفۡسٖ مَّعَهَا سَآئِقٞ وَشَهِيدٞ ٢١ لَّقَدۡ
كُنتَ فِي غَفۡلَةٖ مِّنۡ هَٰذَا فَكَشَفۡنَا عَنكَ غِطَآءَكَ فَبَصَرُكَ ٱلۡيَوۡمَ حَدِيدٞ
٢٢ وَقَالَ قَرِينُهُۥ هَٰذَا مَا لَدَيَّ عَتِيدٌ ٢٣ أَلۡقِيَا فِي جَهَنَّمَ كُلَّ كَفَّارٍ
عَنِيدٖ ٢٤ مَّنَّاعٖ لِّلۡخَيۡرِ مُعۡتَدٖ مُّرِيبٍ ٢٥ ٱلَّذِي جَعَلَ مَعَ ٱللَّهِ إِلَٰهًا
ءَاخَرَ فَأَلۡقِيَاهُ فِي ٱلۡعَذَابِ ٱلشَّدِيدِ ٢٦ ۞ قَالَ قَرِينُهُۥ رَبَّنَا مَآ أَطۡغَيۡتُهُۥ (علامة ربع الحزب ٥٢)
وَلَٰكِن كَانَ فِي ضَلَٰلِۭ بَعِيدٖ ٢٧ قَالَ لَا تَخۡتَصِمُواْ لَدَيَّ وَقَدۡ قَدَّمۡتُ
إِلَيۡكُم بِٱلۡوَعِيدِ ٢٨ مَا يُبَدَّلُ ٱلۡقَوۡلُ لَدَيَّ وَمَآ أَنَا۠ بِظَلَّٰمٖ لِّلۡعَبِيدِ ٢٩
يَوۡمَ نَقُولُ لِجَهَنَّمَ هَلِ ٱمۡتَلَأۡتِ وَتَقُولُ هَلۡ مِن مَّزِيدٖ ٣٠ وَأُزۡلِفَتِ
ٱلۡجَنَّةُ لِلۡمُتَّقِينَ غَيۡرَ بَعِيدٍ ٣١ هَٰذَا مَا تُوعَدُونَ لِكُلِّ أَوَّابٍ حَفِيظٖ
٣٢ مَّنۡ خَشِيَ ٱلرَّحۡمَٰنَ بِٱلۡغَيۡبِ وَجَآءَ بِقَلۡبٖ مُّنِيبٍ ٣٣ ٱدۡخُلُوهَا
بِسَلَٰمٖۖ ذَٰلِكَ يَوۡمُ ٱلۡخُلُودِ ٣٤ لَهُم مَّا يَشَآءُونَ فِيهَا وَلَدَيۡنَا مَزِيدٞ ٣٥



**(16) Haqiqa mun halicci mutum, kuma mun san duk abin da ransa yake faxa masa na wasiwasi da tunani, kuma mu ne muka fi kusa da shi fiye da jijiyar da take wuyansa, wadda take da alaqa da zuciyarsa kai tsaye. (17) A lokacin da Mala'iku guda biyu suke karvar ayyukansa, xayansu yana zaune a damarsa, xayan kuma yana zaune a hagun sa. (18) Babu wata magana da zai faxa face a wurinsa akwai Mala'ika mai kula da abin da yake faxa, kuma wanda yake wurin. (19) Tsananin mutuwa wanda ba hanyar guje masa ya zo da gaskiya, wannan shi ne abin kake guje masa, kake ja baya daga gare shi – Ya kai mutum gafalalle -. (20) Mala'ikan da aka wakilta ya kula da qaho ya yi busa ta biyu a qaho, wannan ita ce ranar alqiyama, ranar da aka yi wa kafirai da masu savo alqawarin narkon azaba. (21) Kowace rai za ta zo tare da ita akwai Mala'ika da yake jan ta, da kuma mala'ika da yake yi mata shaida a kan ayyukanta. (22) Za a cewa wannan mutumin da ake ja: "Haqiqa ka kasance a duniya cikin rafkana ga wannan rana, saboda ruxuwarka da sha'awarka da jin daxinka, amma yau ga shi mun yaye maka rafkanar taka, da abin da kake gani na azaba da baqin ciki, don haka yau ganinka mai kaifi ne, zaka tabbatar da duk abin da ka rafkana ga barinsa. (23) Kuma sai abokin haxinsa daga cikin Mala'ikan da aka wakilta tare da shi ya ce: "Wannan shi ne abin da yake hannuna na ayyukansa, ba tare da ragi ko qari ba". (24) Sai Allah ya cewa Mala'iku guda biyun, wanda ya janyo shi, da kuma mai yi masa shaidar cewa: "Ku wurga duk mai yawan kafirce wa gaskiya, mai taurin kai a cikin wutar Jahannama". (25) Mai yawan hana abin da Allah ya wajabta masa na haqqi, mai yawan qetare iyakar Allah, mai shakka a cikin labari da Allah ya bayar na ni'ima ko na azaba. (26) Shi ne wanda ya sanya wani abin bauta tare da Allah, yana haxa shi da wani a cikin ibada, don haka ku wurga shi cikin azaba mai tsanani. (27) Sai abokin haxinsa daga cikin Shaixanu ya barranta daga gare shi, kuma ya ce: "Ya ubangijinmu ba ni na halakar da shi ba, dama ya kasance a kan vata ga barin gaskiya mai nisa". (28) Sai Allah ya ce: "Kada ku yi husuma a gabana, babu wata fa'ida a kan hakan, na riga na gabatar muku da saqon da Manzanni na suka zo muku da shi na narkon azaba ga wanda ya kafirce min, kuma ya sava min.**

**(29) Ba a musanya magana a gabana, kuma al'qawarina baya savawa, kuma bana zaluntar bayi ta hanyar rage musu ladan kyawawan ayyukansu, ko in qara musu munanan ayyukansu, kaxai dai ina saka musu ne da abin da suka aikata. (30) Ranar da zamu ce da wutar Jahannama: "Shin kin cika da waxanda aka jefa cikinki na kafirai da masu savo?" Sai ta amsawa ubangijinta da cewa: "Shin akwai qari ne?" tana neman qari, saboda ta yi fushi don Ubangijinta. Yayin da Allah ya ambaci narkon azaba ga kafirai, sai kuma ya ambaci tanadin da ya yi wa bayinsa Muminai, ya ce: (31) Kuma aka kusanto da Aljannah ga masu tsoron ubangijinsu, ta hanya kamanta umarninsa, da nisantar haninsa, su ga abin da yake cikinta na ni'imomi kusa da su, ba da nisa ba. (32) Kuma za a ce da su: "Wannan shi ne abin da Allah ya yi alqawari ga duk wani mai yawan komawa ga Ubangijinsa da tuba, kuma mai kiyaye abin da Ubangijinsa ya lazimta masa. (33) Wanda ya ji tsoron Allah a voye, a inda babu mai ganinsa sai Allah, kuma ya haxu da Allah yana mai lafiyayyar zuciya, mai fuskantar Allah, kuma mai yawan komawa gare shi. (34) Kuma za a ce da su: "Ku shiga Aljannah kuna masu kasancewa cikin aminci daga duk wani abin qi, wannan ita ce ranar da za a dauwama, wadda babu qarewa daga gare ta har abada". (35) Suna da duk abin da suke so a cikinta, na ni'imar da bata qarewa, kuma a wurinmu akwai qarin wasu ni'imomin, waxanda idanu basu tava gani ba, kunne kuma bai tava jin labarinsu ba, kuma bai tava xarsuwa a zuciyar wani mutum ba, daga ciki akwai ganin Allah.**

**Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa: 1 - Allah ya san duk abin da yake xarsuwa a cikin zukata, na alheri ko na sharri. 2 - Haxarin rafkana ga ranar lahira. 3 - Tabbatuwar siffar adalci ga Allah Maxaukakin sarki.**

وَكَمۡ أَهۡلَكۡنَا قَبۡلَهُم مِّن قَرۡنٍ هُمۡ أَشَدُّ مِنۡهُم بَطۡشٗا فَنَقَّبُواْ
فِي ٱلۡبِلَٰدِ هَلۡ مِن مَّحِيصٍ ٣٦ إِنَّ فِي ذَٰلِكَ لَذِكۡرَىٰ لِمَن
كَانَ لَهُۥ قَلۡبٌ أَوۡ أَلۡقَى ٱلسَّمۡعَ وَهُوَ شَهِيدٞ ٣٧ وَلَقَدۡ خَلَقۡنَا
ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلۡأَرۡضَ وَمَا بَيۡنَهُمَا فِي سِتَّةِ أَيَّامٖ وَمَا مَسَّنَا
مِن لُّغُوبٖ ٣٨ فَٱصۡبِرۡ عَلَىٰ مَا يَقُولُونَ وَسَبِّحۡ بِحَمۡدِ رَبِّكَ
قَبۡلَ طُلُوعِ ٱلشَّمۡسِ وَقَبۡلَ ٱلۡغُرُوبِ ٣٩ وَمِنَ ٱلَّيۡلِ فَسَبِّحۡهُ
وَأَدۡبَٰرَ ٱلسُّجُودِ ٤٠ وَٱسۡتَمِعۡ يَوۡمَ يُنَادِ ٱلۡمُنَادِ مِن مَّكَانٖ قَرِيبٖ
٤١ يَوۡمَ يَسۡمَعُونَ ٱلصَّيۡحَةَ بِٱلۡحَقِّۚ ذَٰلِكَ يَوۡمُ ٱلۡخُرُوجِ ٤٢ إِنَّا
نَحۡنُ نُحۡيِۦ وَنُمِيتُ وَإِلَيۡنَا ٱلۡمَصِيرُ ٤٣ يَوۡمَ تَشَقَّقُ ٱلۡأَرۡضُ
عَنۡهُمۡ سِرَاعٗاۚ ذَٰلِكَ حَشۡرٌ عَلَيۡنَا يَسِيرٞ ٤٤ نَّحۡنُ أَعۡلَمُ بِمَا يَقُولُونَۖ
وَمَآ أَنتَ عَلَيۡهِم بِجَبَّارٖۖ فَذَكِّرۡ بِٱلۡقُرۡءَانِ مَن يَخَافُ وَعِيدِ ٤٥

ترتيبها ٥١ سُورَةُ الذَّارِيَاتِ آياتها ٦٠

بِسۡمِ ٱللَّهِ ٱلرَّحۡمَٰنِ ٱلرَّحِيمِ

وَٱلذَّٰرِيَٰتِ ذَرۡوٗا ١ فَٱلۡحَٰمِلَٰتِ وِقۡرٗا ٢ فَٱلۡجَٰرِيَٰتِ يُسۡرٗا ٣
فَٱلۡمُقَسِّمَٰتِ أَمۡرًا ٤ إِنَّمَا تُوعَدُونَ لَصَادِقٞ ٥ وَإِنَّ ٱلدِّينَ لَوَٰقِعٞ ٦



**36 Al'ummun da muka halakar gabanin
waxannan mushirikai masu qaryatawa na garin
Makkah suna da yawa, kuma sai da suka bincika
garuruwa ko zasu samu wurin vuya, ko matserata
daga azaba, amma basu samu ba. 37 Haqiqa a
cikin wannan abin da aka ambata, na halakar da
al'ummun da suka gabata akwai tunatarwa da
wa'azi ga mai zuciyar da yake hankaltuwa da ita,
ko kuma ya sauraroa da jin sa, tare da halarto da
zuciyarsa, ba tare da ya rafkana ba. 38 Haqiqa
mun halicci sammai, kuma muka halicci qasa, da
abin da yake tsakanin sammai da qassai, duk a
cikin kwanaki shida, duk da cewa muna da ikon
halittarsu a xan qanqanin lokaci, kuma babu wata
gajiya da ta same mu, kamar yadda Yahudawa
suke faxa. 39 Ya kai wannan Manzo, ka yi haquri
a kan abin da Yahudawa da wasunsu suke faxa,
kuma ka yi sallah ga Ubangijinka, kana mai yi
masa godiya - sallar asuba - gabanin hudowar
rana, kuma ka sallaci la'asar gabanin faxuwarta.
40 Daga wani yanki na dare ka yi sallah ga
Ubangiji, kuma ka tsarkake shi bayan kammala
salloli. 41 Ya kai wannan Manzo, ka saurari ranar
da Mala'ikan da aka wakilta ya yi busa a qaho,
busa ta biyu, zai yi kira daga wuri makusanci.
42 Ranar da halittu zasu ji tsawar tashin
alqiyama da gaskiyar da babu kokwanto a
cikinta. Wannan ranar da zasu ji wannan tsarwar
ita ce ranar fitowar matattu daga qaburburansu,
domin fuskantar hisabi da sakamako.
43 Tabbas mune muke rayawa, kuma mune
muke kashewa, babu mai rayawa sai mu, kuma
babu wanda yake kashewa wanda ba mu ba, kuma gare mu kaxai bayi zasu koma ranar alqiyama, domin fuskantar
hisabi da sakamako. 44 Ranar da qasa zata kekkece musu, sai su fito daga cikinta suna masu gaggawa. Wannan
tara bayin lamari ne mai sauqi a wurinmu. 45 Mune mafiya sanin abin da waxannan masu qaryatawa suke faxa,
kai kuma wannan Manzo ba mai tilasta musu ba ne a kan imani, kai mai isar da abin da Allah ya umarceka ka isar
ne, don haka, ka tunatar da wanda yake tsoron azabata a kan kafirai da masu savo da Alqur'ani, domin mai jin
tsoro shi ne kaxai yake wa'azantuwa, kuma yake tunawa idan an tunatar da shi.**

# Suratuz Zariyat

An Saukar Da Ita A Makkah

**Daga Manufofin Surar:** **Sanar da talikai haqiqanin da inda arzikinsu yake zuwa, shi ne Allah Maxaukakin Sarki, saboda su gudu zuwa gare shi, su tabbatar da bauta a gare shi.**

**Tafsir:** **1 Allah yana yin rantsuwa da iskoki masu sheqar da qasa.**
**2 Da kuma giragizai masu xauke da ruwan sama mai yawa.**
**3 Da kuma jiragen ruwa masu gudu a kan teku cikin sauqi.**
**4 Da kuma Mala'iku waxanda suke rarraba abin da Allah ya yi musu umarni su raba na daga al'amuran bayi.**
**5 Haqiqa alqawarin da Ubangijinku yake yi muku na hisabi da sakamako gaskiya ne, babu kokwanto a cikinsa.**
**6 Kuma haqiqa hisabin bayi tabbatacce ne a ranar alqiyama, ba makawa.**

**Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:** **1 - Yin izina da abubuwan da suka faru a cikin tarihi aiki ne na ma'abota zukatan da suke kiyaye abubuwa. 2 - Allah ya halicci duniya a cikin kwanaki shida, don wasu hikimomi da shi ne ya san su, wataqila daga cikinsu akwai tsarin aiwatar da a'lamura sannu- sannu. 3 - Rashin ladabin Yahudawa wajen siffata Allah da gajiya bayan ya halicci sammai da qassai. Wannan kafircewa Allah ne.**

وَٱلسَّمَآءِ ذَاتِ ٱلۡحُبُكِ ۝٧ إِنَّكُمۡ لَفِي قَوۡلٖ مُّخۡتَلِفٖ ۝٨ يُؤۡفَكُ عَنۡهُ مَنۡ
أُفِكَ ۝٩ قُتِلَ ٱلۡخَرَّٰصُونَ ۝١٠ ٱلَّذِينَ هُمۡ فِي غَمۡرَةٖ سَاهُونَ ۝١١ يَسۡـَٔلُونَ
أَيَّانَ يَوۡمُ ٱلدِّينِ ۝١٢ يَوۡمَ هُمۡ عَلَى ٱلنَّارِ يُفۡتَنُونَ ۝١٣ ذُوقُواْ فِتۡنَتَكُمۡ
هَٰذَا ٱلَّذِي كُنتُم بِهِۦ تَسۡتَعۡجِلُونَ ۝١٤ إِنَّ ٱلۡمُتَّقِينَ فِي جَنَّٰتٖ وَعُيُونٍ
۝١٥ ءَاخِذِينَ مَآ ءَاتَىٰهُمۡ رَبُّهُمۡۚ إِنَّهُمۡ كَانُواْ قَبۡلَ ذَٰلِكَ مُحۡسِنِينَ ۝١٦
كَانُواْ قَلِيلٗا مِّنَ ٱلَّيۡلِ مَا يَهۡجَعُونَ ۝١٧ وَبِٱلۡأَسۡحَارِ هُمۡ يَسۡتَغۡفِرُونَ ۝١٨
وَفِيٓ أَمۡوَٰلِهِمۡ حَقّٞ لِّلسَّآئِلِ وَٱلۡمَحۡرُومِ ۝١٩ وَفِي ٱلۡأَرۡضِ ءَايَٰتٞ
لِّلۡمُوقِنِينَ ۝٢٠ وَفِيٓ أَنفُسِكُمۡۚ أَفَلَا تُبۡصِرُونَ ۝٢١ وَفِي ٱلسَّمَآءِ رِزۡقُكُمۡ
وَمَا تُوعَدُونَ ۝٢٢ فَوَرَبِّ ٱلسَّمَآءِ وَٱلۡأَرۡضِ إِنَّهُۥ لَحَقّٞ مِّثۡلَ مَآ أَنَّكُمۡ
تَنطِقُونَ ۝٢٣ هَلۡ أَتَىٰكَ حَدِيثُ ضَيۡفِ إِبۡرَٰهِيمَ ٱلۡمُكۡرَمِينَ ۝٢٤ إِذۡ
دَخَلُواْ عَلَيۡهِ فَقَالُواْ سَلَٰمٗاۖ قَالَ سَلَٰمٞ قَوۡمٞ مُّنكَرُونَ ۝٢٥ فَرَاغَ إِلَىٰٓ
أَهۡلِهِۦ فَجَآءَ بِعِجۡلٖ سَمِينٖ ۝٢٦ فَقَرَّبَهُۥٓ إِلَيۡهِمۡ قَالَ أَلَا تَأۡكُلُونَ
۝٢٧ فَأَوۡجَسَ مِنۡهُمۡ خِيفَةٗۖ قَالُواْ لَا تَخَفۡۖ وَبَشَّرُوهُ بِغُلَٰمٍ عَلِيمٖ ۝٢٨
فَأَقۡبَلَتِ ٱمۡرَأَتُهُۥ فِي صَرَّةٖ فَصَكَّتۡ وَجۡهَهَا وَقَالَتۡ عَجُوزٌ عَقِيمٞ
۝٢٩ قَالُواْ كَذَٰلِكِ قَالَ رَبُّكِۖ إِنَّهُۥ هُوَ ٱلۡحَكِيمُ ٱلۡعَلِيمُ ۝٣٠



**(7) Kuma Allah yana yin rantsuwa da sama mai
kyakkyawar halitta, wadda take da hanyoyi.
(8) Haqiqa ku - Mutanen Makkah - tabbas kuna
cikin maganganu masu cin karo da warware
juna. Wani lokacin kuna cewa: "Alqur'ani tsafi
ne". Wani lokacin kuma ku ce: "Waqe ne" Wani
lokaci kuma ku ce: "Muhammad mai sihiri ne"
Wani lokaci kuma ku ce: "Mawaqi ne".
(9) Ana kawar da wanda aka tsara za'a kawar da
shi daga barin yin imani da Alqur'ani da kuma
Annabi (S.A.W) domin Allah ya san ba zai yi
imani ba, don haka ba a datar da shi ga shiriya.
(10) An tsinewa waxannan masu qaryatawa,
waxanda suke faxi maganganun da suka ga dama
a kan Alqur'ani da Annabinsu.
(11) Waxanda suke cikin jahilci da rafkana ga
gidan lahira, basu damu ba da ita ba.
(12) Suna tambaya cewa: "Yaushe ne ranar
sakamakon?". Amma basa yin aiki don wannan
ranar. (13) Sai Allah ya amsa musu tambayar su
da cewa: "Ita ce ranar da za a azabtar da su a
cikin wuta". (14) Za a ce musu: "Ku xanxani
azabarku, wadda kuka kasance kuna roqon a
gaggauto muku da ita, yayin da Manzanninku
suke yi muku gargaxi da ita, kawai saboda izgili".
(15) Haqiqa masu tsoron Ubangijinsu, ta hanyar
kamanta umarninsa, da nisantar haninsa, a
ranar alqiyama suna cikin Aljannatai da qoramu
ke gudana a cikinsu. (16) Suna masu samun
sakamako mai girma da Ubangijinsu ya basu.
Haqiqa sun kasance gabanin wannan sakamako
mai girma masu kyautatawa a duniya.
(17) Sun kasance suna yin sallah a cikin dare, basa
yin bacci sai xan lokaci kaxan. (18) Kuma a lokacin
da alfijir ya kusa ya keto suna neman gafarar
zunubansu a wurin Allah. (19) Kuma a cikin dukiyoyinsu akwai wani haqqi – na sa kai - da suke bawa mai roqo daga
cikin mutane, da wanda ma baya roqonsu, daga waxanda ba a bawa arziki ba. (20) A bayan qasa da abin da Allah ya
sanya a kanta na duwatsu, da tekuna, da qoramu, da bishiyoyi, da tsirrai, da dabbobi, akwai dalilai da suke nuna
ikon Allah, ga masu sakankancewa Allah shi ne mai halitta, mai surantawa. (21) A cikin kawunanku – Ya ku Mutane
- akwai dalilai suke nuna ikon Allah, Yanzu shin ba kwa gani ne ku xau izina?. (22) Kuma a cikin sama arzikinku na
duniya da na addini yake, kuma a cikinta ne abin da ake yi muku alqawari na alheri da sharri yake. (23) Na rantse
da Ubangijin sammai da qassai tashi bayan mutuwa gaskiya ne, babu kokwanto a cikinsa, kamar yadda babu
kokwanto a cikin furucinku, lokacin da kuke yin sa. (24) Ya kai wannan Manzo, shin labarin baqin Annabi Ibrahim
daga cikin Mala'iku yazo maka? Su ne baqinsa waxanda ya karrama su. (25) Lokacin da suka shigo wurinsa, suka
ce masa: "Aminci ya tabbata a gare ka" Sai Annabi Ibrahim ya mayar musu da cewa: "Aminci ya tabbata a gare
ku". Sannan ya faxa a cikin ransa ce: "Waxannan kuma wasu mutane, ba mu san su ba". (26) Sai ya juya zuwa ga
iyalansa a voye, sai ya zo musu da xan maraqi cikakke mai qiba guda (Soyayye ko dafaffe). Yana zaton mutane ne.
(27) Ya gabatar da wannan xan maraqin gare su, ya yi musu magana cikin tausasawa ya ce: shin ba zaku ci abin da
aka kawo muku na abinci ba?". (28) Da ya ga basu ci ba, sai zuciyarsa ta fara tsoronsu, da suka fahimci hakan, sai
suka ce da shi – suna masu kwantar masa da hankali -: "Kada ka ji tsoro, mu 'yan aike ne daga wurin Allah" suka
bashi labarin abin da zai faranta masa rai, shi ne za a haifa masa yaro mai ilimi da yawa. Wannan yaron da aka yi
masa bushar da samu shi ne Annabi Is'haq (A.S). (29) Yayin da matarsa ta ji busharar, sai ta nufo wurinsu tana xaga
murya saboda farin ciki, kuma ta mari fuskarta, ta ce cikin mamaki: "Ashe tsohuwa tana haihuwa, alhali asali ma
bakarara ce (bata haihuwa)!". (30) Sai Mala'iku suka ce mata: "Abin da muka baki labari, Ubangijinki ne ya faxa,
kuma duk abin da ya faxa babu mai hanawa. Haqiqa shi mai hikima ne a cikin halittarsa, da gudanarwar sa, kuma
masanin halittarsa da abin da ya dace da su ne".**

**Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa: 1 - Kyautata aiki da kuma yin sa don Allah,
sababi ne na shiga Aljannah. 2 - Falalar tsayuwar dare, kuma tana cikin mafi ladan ibadu. 3 - Yana daga laduban
saukar baqi abubuwa masu zuwa: amsa sallama da mafi kyawun wadda aka yi maka, da shirya abinci a voye, da yi
wa baqin tanadi tun kafin su sauka, da rashin togace wani abinci daga abincin baqi, da tsayawa da kai wajen shirya
komai, da yin gaggawa wajen hakan, da gabatar musu da abincin, da yi musu magana cikin tausasawa.**